Cikin gaggawa kuwa suka yi mata abinda ya dace shaɗaya saura na dare ta farka da shaƙuwa da sauri suka yi kanta a hankali take buɗe idanuwanta har tayi nasaran buɗe su tar tana kallon Maman su murya a hankali irin na masu jin jiki tace "Ruwa" Daga haka tayi shuru tana kallo Fiddoh wacce ita ma kallon ta take cike da jin daɗi ganin ta farka cikin hankalin ta. "Sannu Nuriyya Ubangiji ya baki lafiya" Lumshe ido kawai tayi tare da karɓan ruwan ɗumin da Maman su take bata cije bakinta tayi jin yanda ƙasanta ke mata raɗaɗin bala'i "Zanyi fitsari" Da sauri Maman su ta ɗauko ɗan bokiti sai dai ta rasa yadda zata yi ta taimaka mata dole sai da suka kira nurse "Wash Allah!" Ta faɗa tare da damƙe zanin gadon saboda azaban zafin da take ji. Ko nishi mai ƙarfi tayi tana jin azaba bare kuma magana hawaye ne ya shiga wanke mata fuska duk da fitsarin da take ji da ƙyar ta iya yin kaɗan mai haɗe da jini saboda ɗinkin dake jikinta.

Haka suka zauna jugum babu mai magana a cikin su da sassafe sai ga ƴan Sanda da wani lawyer gwabnati sun zo ɗaukar ta domin zasu mata wasu tambayoyi kasancewar Hajiya Larai ta cika ƴan Sandan da kuɗi ana ta ƙoƙarin ture file ɗin ta shuru tayi tana kallon lawyer dake mata tambayoyi take taji numfashin ta na shirin barin jikinta sakamakon kunnuwanta dake jiyo mata muryan wadda yake gindaya mata kashedi a kan muddin ta kuskura ta faɗa wani abu sai sun mata abinda ya fi haka.

Girgiza kai tayi tana faɗin "Ban san su ba" Lawyer yace "Ki ƙara zurfafa tunani dai.." Kallon ta ya yi ganin tayi shuru taƙi tanka masa "Yarinya kinyi nazari domin a ƙwato miki ƴancin ki.." "Yallaɓai tun da tace bata san su ba a ƙyale maganar zai fi" Zai yi magana Maman su ta sake faɗin "Dan Allah karka ce komai a hakan ma mun gode!" Dagewa yai a kan lallai Nuriyya ta faɗi wani abun ƙarshe jikinta ne ya fara rawa nan ta shiga jijjiga lamarin ya tsananta sosai domin likitotin sunyi faɗa  sosai  da cewan bai dace daga farkawan ta a tsitsiye ta da tambayoyi ba.

Rai a ɓace Fiddoh ta nufi ofishin ƴan sanda domin jin dalilin da yasa aka rufe file ɗin Nuriyya sai dai bata samu damar shiga ba, Domin yadda ta dinga zaginsu tana tsine musu abinda ya haddasa ƙaramin rigima tsakaninsu kenan tayi kuka tare da jin baƙin cikin abinda aka aikata musu. Wato a duniyar nan talaka ba komai bane idan abu ya haɗaka da ƴaƴan masu kuɗi in baka da mai tsaya maka sunan ka sorry abinda ya faru da Nuriyya kenan duk yadda Fiddoh ta so a dawo da case ɗin abin bai yuwu ba. Haka ta dawo asibitin nan ta kuma tarar da sabon tashin hankali domin jini ne yake zuba mata sosai tana jin azaba sosai idan ta zo fitsari gashi dai tana jin fitsarin amma bata iyawa sai dai kaɗan ya fito dalilin da yasa ta firgicewa tare da ficewa cikin hayyacinta kenan. Gashi ana buƙatar ƙarin magungunan dan ga kuɗin aikin da wasu alluran da ake buƙata. Bata da yadda zata yi domin tana son ƴar'uwarta tana son ganin ta dawo kamar yadda mutane suke duk da a kullum cikin faɗa da rigima suke akan irin rayuwar da Firdausin take yi hakan bai hanasu soyayya da shaƙuwa irin na ƴan'uwan juna ba.

Basu da wani mataimaki sai Allah dan Baban su ma maganan banza yake faɗa domin ƙwandalan shi yaƙi bayarwa. Babu irin taimakon da bata nima ba sai dai kowa yace idan ta amince ayi ban gishiri in baka manɗa dake basu da ƴan'uwa a gari dan Babansu da Maman su mutanen Sudan ne cirani ya kawo su Nigeria. Sai da Likitan ya more ta na kwana uku kafin ya

yarda ya duba Nuriyya inda aka mata aiki.
***
"Wallahi Alhaji iya bincike nayi amma ban samo inda yarinyar take ba" Kallon mutumin Hon. Sa'id yai tare da faɗin "Ko sunanta baka sani ba?" Gyaɗa mishi kai ya yi "Ok zaka iya tafiya mun gode" Kallon Aminu yai yana faɗin "Muje ko?" Cike da takaicin kalamansa Alhaji Aminu yace "Muje ina bayan ban ganta ba?" Gyara tsayuwa Hon. Sa'id yai yana faɗin "Mun kai sati muna jele a nan amma babu labarin ta ina ga babu amfanin tsayuwar ta mu tun da ko mun tsaya ɗin ba zuwa zatayi ba waya sani ma ko aure tayi..." Wani irin kallo Alhaji Aminu yai masa tare da runtsa idanunsa yana jin kalmar auren nan na dukan zuciyar shi. Da yasan haka zai kasance da tun farko ya faɗa mata abinda ke ran shi. Bai san ya kamu da mugun ƙaunarta ba sai yanzun da ya nime ta ya rasa tayi ɓatar damo babu ita babu labarin ta, Abun takaici ma ko sunanta bai sani ba, Dole suka dawo gida amma gabaɗaya ba shi da nutsuwar zuciyar haka kawai sai yana ji a ran shi kaman ba lafiya ba.

Matarshi ta lura da yanayin nasa sai dai bata wani damu ba. Ta mayar da hankalinta ga kasuwancin tare da ƙoƙari tura Hisham Ƙasar waje domin tun da wannan lamarin ya faru shi ma a firgice yake shi yasa take son tura shi can yaje ya ƙarasa karatun sa babu ɓata lokaci kuwa ta gama mishi duk wasu abubuwan da ya kamata na tafiya waje inda yai sallama da abokansa tare da Hajiya Umma suka nufi airport sai da suka ga tashin jirginsu sannan suka dawo gida.

Lamarin Alhaji Aminu kuwa abun ya babu daɗi domin har ƴar jinya sai da yai na kwana biyu Amininsa ne yake sanar da Umma abinda ya haddasa masa wannan damuwar taji matuƙar mamakin jin dalilin rashin lafiyar nasa "Allah mai iko Aminu yanzun da girman ka soyayya tayi maka irin wannan kamun? Ɓatan basira ɗaya da ku kayi na rashin sanin sunanta da inda take da an san wannan bayanan da komai yazo da sauƙi amma duk da haka ka yawaita Addu'a idan rabon ka ce In Sha Allah zaka same ta, In kuma ba rabon ka bace Ubangiji ya musanya maka da mafi alheri.." Da sauri ya tari Numfashin ta gurin faɗin "In Sha Allah rabo nace" Murmushi kawai tayi domin lamarin na shi har mamaki ya bata wai Aminu yake kwance a kan SO? Duk wannan wainar da ake toyawa matar shi bata sani ba, domin har ya gama kwanciyarshi a asibiti bata leƙo shi ba. Suhaima ce kawai ke kaiwa da komowa a asibiti.

Kwana biyu kenan da a ka sallamosu daga asibiti sai dai abin sakawa a bakin Salati na niman fin ƙarfin su ga Nuriyya ma jikin sai a hankali dan bata iya wani ƙwaƙƙwaran motsi tana daga kwance ɗan aikin da Maman su take ma yanzun babu domin Hajiya Larai koran ta tayi a kan kwana biyu bata zo ba, Duk da ta faɗa mata dalilin rashin zuwan nata haka matar nan ta baɗawa idanunta toka ta kore ta.
Ɗan tallar da Zaliha take Nuriyya ta hana ta domin tsoron abinda ya faru da ita ya faru kan ƴar'uwarta take ji. Ga Baban Su ba taimaka musu yake ba abinda Maman su ta ɗan nimo ta dafa musu ma ƙoƙarin cinyewa yake duk da takaici halinshi jikin Nuriyya yake daɗe taɓarɓarewa gashi kullum bashi da magana wadda ya wuce ta miƙe taje ta nimo mijin aure ko kuma ya yi sadaka da ita lamarin babu daɗi domin tana cikin ƙuncin rayuwa dole aikatau Maman su ta koma a yanzun dai Fiddoh ce ke ƙoƙarin samo musu abinda zasu ji duk da kullum sai sunyi daru da Nuriyya take karɓan abincin "Idan baki ci ba taya zaki sha magani? Ni kaina

ba son rayuwar nan nake ba babu yadda na iya ne kawai Dan Allah Nuriyya ki daure ko dan ki sha magani saboda ki samu lafiyan jikin ki bana jin daɗin ganin ki kwance"

Da ire-iren waɗannan kalaman take samu taci abincin haka rayuwa taci gaba da tafiya da daɗi ba daɗi haka suka dinga haƙuri dake Allah ya basu jajirtacciyar uwa sai abubuwan suka fara musu sauƙi aiki ba irin wanda ba tayi dan samun abinda zasu ci sai dai kuma kwatsam watarana suka tsinci kansu cikin halin rashi na ƙaramar ƙanwarsu Nafisa lamarin da yayi sanadiyar rugujewar ɗan farincikin da suka samu nan komai ya sake kwaɓewa.
Sannu a hankali rayuwa ta fara juya musu baya domin wani irin rashin lafiya da Fiddoh ta kwanta ganin abu goma da ashirin ya haɗu ma Maman su ne yasa Nuriyya dauriya ta fara ƙarfafama kanta gwiwa domin wacce take ɗan taimakon nasu gata kwance.

*Wannan littafin kuɗi ne domin kasance cikin group zaki/zaka tura ₦500 ta wannan account 2389596965 Aisha jubreel Zenithbank sai a turawa wannan Number shedar biya 09079740079 Please Idan ba siyan littafi za kiyi ba karki ɓatawa kan ki lokaci gurin min magana*
[5/9, 11:42 PM] FARHATULKALB💔🤗: *_♡AMNOOR...!_*
_A Romantic Story_

®
FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION📚
★F. W. A★

Free page 17_18

*H-P Place Group*

"Ki yi haƙuri Nuriyya ta ko wanne yanayi Ubangiji ya kan jarabci bawa domin ya gwada ƙarfin imaninsa ta ki ƙaddarar kenan babu ta yadda za ki kauce masa Allah ya ƙara miki lafiya da sannu za ki ga sakayya akan duk wanda ya aikata miki wannan aika-aikar, me ya sa ba ki kira number dana ba ki ba? Yanzu da ban biyo Na'ilah duba ƙawarta ba shi kenan ba zan san abin da ke faruwa da ke ba? Har yanzun kin kasa sakin jikinki da ni bayan da zuciya ɗaya nake ƙaunar ki, Allah ne shaida"
Sunkuyar da kai Nuriyya ta yi tana jinjina irin ƙaunar da Amrah take mata "Na gode sosai Amrah!" Hannunta ta riƙe tana faɗin "In Sha Allah zan tsaya miki a dawo da case ɗin.." Cire hannunta ta yi daga nata tana faɗin "In har da gaske ƙaunar da kike min daga zuciyarki ce dan Allah kar ki ɗaga wannan maganar koma waye na yafe!" Ta ƙarasa maganar tare da ɗauke hawayen da ke zubo mata "Shi kenan ba zan tada maganar ba tun da ba ki so zamu wuce ki riƙe wannan zamu dinga magana" Kallon waya tare da tulin kuɗin ta yi da sauri Maman su ta ce "Amratu! Wannan kayan arziki haka? Ubangiji ya yi albarka mun gode ƙwarai!" Murmushi Na'ilah ta yi sanan ita ma ta miƙawa Fiddoh kuɗi tare da ajiye mata jakar da ta zo musu da shi wanda yake ɗauke da kayan abinci "Beb! Ki yi ƙoƙari ki miƙe Please ana ta cigiyarki kowa ya yi missing ɗin ki duk casu idan babu ke ba daɗi wallahi gashi kwana biyu ba wani update tun

bayan na Alh. Aminu bamu sake fitar da komai ba, after zan dawo tare da Dr ya duba mana ke" Gyaɗa mata kai Fiddoh ta yi tare da faɗin "Thank you Bestie!"
Bayan tafiyarsu Maman su ta kalli kuɗi haɗe da kayan tana jinjina lamarin a zuciyarta ashe har yanzu akwai mutane irin Alh. Aminu a duniyarnan? Zaliha ce ta katse mata tunani ta hanyar faɗin "Wayyo Allah daɗi kashe ni! Allah yai musu albarka yanzun Mamanmu tun da kin iya turare Allah a ware wasu kuɗin ki faɗa min abubuwan da za a sayo sai ki fara yi kawai kuma a duba mana wani ɗaki daban kinga da ma nan ya yi kaɗan wlh tsawon shekaru muna zaune a ɗaki ɗaya yanzu ka a ware mana namu." Maman Nafisa ta ce "Kin yi gaskiya, amma ina tsoron kar Babanku ya zo ya ɗauke kuɗaɗen dan wallahi muddin ya shigo na san sai ya ga wannan kuɗin.."
"Aikuwa bai isa ya je inda kuɗin nan suke ba, wallahi muddin ya taɓa zan yi mishi rashin M.." Fiddoh ta faɗa tana gyara kwanciyarta.
Da yamma kuwa sai ga Na'ilah ta dawo tare da likita nan ya shiga duba jikinta sannan ya bata magungunan haɗe da allurai bata ƙyale likitan ya ta fi ba sai da ta sa shi ya duba jikin Nuriyya.
Kwana biyu tsakani Fiddoh ta miƙe ta fito ras da ita nan ta tsaya ta ƙarewa matan gidan kowacce sai da ta zageta sannan ta fita ta nufi gurin Emanuel da ma a takure take daga nan ne fa lamarin ya canza salo nan suka faɗa duniyar masha'arsu Fiddoh kamar mayya haka ta kanannaɗeshi suna abu ɗaya sai da ta fanshe kwanakin da basu tare sannan ta ƙyale shi tana kwance saman jikinshi tana murza nipples ɗinsa cikin yanayin da ke nuna har yanzu bata samu gamsuwar da take buƙata ba, hannunta ya riƙe yana magana cin Hausar da be gama ƙwarewa.
"Mene kuma Fiddoh? Na yi sosai ki bari na huta haka.." Wani irin numfashi ya ja sakamakon kamo bananarshi da ta yi tana matse saman "Hmmm!" Ya sauke wani gwauron numfashi yana jin yadda take tsotsar abin sai da ta sa suka koma tana ride ɗin shi kamar ba za ta ƙyale shi ba.
Sai da ya ga abin nata na neman fin ƙarfin shi kafin ya ƙwace daga jikinta yana mayar da numfashi duk da shi ya fara buɗe mata ido amma ya lura jarabarta ya fi ƙarfin sa. Kallon sa ta yi tana yamutsa fuska sannan ta shirya ta fita.
Bayan ta karɓi dubu biyar gurinshi domin yanzu rashin mutunci take ji.

Tana fitowa suka yi karo da Baban su dakatawa ta yi tana ƙare mishi kallo ganin yadda ya sha shadda me ruwan goro sai maiƙo yake ga dukkan alamu sabo ne kallon takalmin ƙafarshi ta yi nan ma dai sabo ne hatta agogon hannunsa. "Allah ya sa dai ba kayan wasu aka ƙwamuso ba, dan na ji ana sanar da cewa an yi sata.." Hannunsa da ya miƙo mata ne ya sa ta katse maganar tata alamu yai mata akan ta ba shi na shi kason "Wallahi ba zan ba da ba! Domin gumi na ne, yadda kake buga jiki kake ɗauke-ɗauke haka ni ma nake sake jiki na yi abin da za a ba ni kuɗi.."
"Au haka ne abun?" Cike da baƙin cikin halinsa ta ce " Ya fi haka, lokacin da nake kwance me ka tsinana min? Mamanmu ke ɗawainiya da mu ita ce take fita tana yawo a rana domin samo mana abin da za mu ci.."
"Ba za ki ba ni ba kenan?" Tsaki ta ja sannan ta ce. "Muje na gwada idan ya mun sai na ba ka." Tana gama faɗar haka tai shigewarta ba tare da ta ba shi ko sisi ba.
Komawa yai gun Ema yana tambayar shi yau bata shawu ba ne? "Ta sha amma ba sosai ba" Gyaɗa kai ya yi tare da miƙa ma sa hannu "Mene ne kuma?" Emanuel ya tambaye shi tare da ɓata fuska. "Money! Ai na faɗa maka duk lokacin da kuka yi wata mu'amula ina da nawa kason ɗiyata ce, ni na ba ka go and hed ɗin da kake kome da ita" 2k ya zaro ya ba shi. Lokacin da ta

shiga gidan direct ta nufi ba yi bayan ta ɗauki ƙaton butar da Maman Nafisa take alwala da shi kallon Zaliha da ke girki ta yi sannan ta ce "Ki kawo min ruwan zafi" Taɓe baki Zaliha ta yi sannan ta ɗibi ruwan tabi bayan ta da shi.
Washegari bayan fitar ta sai gata ita da su Na'ilah da leda niƙi-niƙi cike da kaya ta direwa Maman Nafisa tana faɗin "Kayan haɗin turaren na kawo miki tare da haɗin gwiwar 'yan group ɗin mu" Cike da mamaki Maman Nafisa ta ce "Wani group kenan?" Dariya suka yi sannan suka fita Fiddoh tana faɗin "Group ɗin 'yan sirri masu tona asirin abin da ba'a sani ba" Wani iri take jin abun, daɗi ne ba daɗi ba, rayuwar da Fiddoh take yi sam bata so babu yadda za ta yi, ka haifi ɗa ne ba ka haifi halinsa ba, mutane da yawa suna mata kallon uwar da 'yarta ta gagare ta bayan kuma ba haka ba ne, da ana buɗe zuciya da ta buɗe kowa ya ga irin baƙin cikin da ke ciki wanda ya danganci halin da Firdausi take yi, duk iya ƙoƙarin da Uwa take Allah ya gani ta yi shi amma abun sai dai a barwa Ubangiji...
"Ki yi haƙuri Mama addu'a za ki ci gaba da yi mata. Komai yana da ƙarshen sa haka watarana zai zamto tamkar ma ba a yi sa ba". Cewar Zaliha, ɗauke hawayen da ke zubo mata ta yi tare da faɗin. "Haka ne Zaliha Ubangiji ya daɗe shirya mana zuri'a." Amsawa ta yi sanna ta kwashe kayan ta je ta adana su. "Mama!" Juyowa ta yi tana kallon Zaliha. "Na'am Zaliha ina sauraron ki."
"Da ma na ce yaushe za ki fara yin turaren? Dan na faɗawa Malaman islamiyyan mu zan kawo musu su saya kuma ma na ce da ƙawaye na su faɗa a gida.." Shuru ta yi ganin Maman Nafisa tana murmushi "Tun ba a fara ba har kin soma tallar?"
"Ai da zafi-zafi akan bugi ƙarfe in ji masu salon zance" Miƙewa Maman Nafisa ta yi tana faɗin.
"Ai da ma sai masu salon zance dan Hausar ma jinsa muka yi, zan yi ƙoƙari na fara amma fa gaskiya bana son maganar tallar nan domin na riga na yanke shawarar na fita da shi..." Cikin shagwaɓa ta katse mata maganar "Haba Mamanmu! Bafa tallar ba ne, iya makaranta ne fa dan Allah kin ji Allah daga makaranta shi kenan" Da ƙyar dai ta lallaɓa Maman su ta yarda akan in ta yi zata bata ta je da shi. Duk wannan budurin da ake Nuriyya tana daga kwance tana sauraron su ba tare da ta ce komai ba.
Domin har yanzun jikin nata ya kan motsa mata, cikin kayan da Na'ilah ta kawo musu suka yi dafa dukan taliya suka ci su uku domin Fiddoh bata dawo ba, suna cikin cin abincin Baban su ya shigo shi ma suka zuba mishi sai da ya gama ci sannan ya tambaye ta inda ta samu kayan turare shuru ta yi masa ba tare da ta yi bayani ba. Nuriyya ya dakawa tsawa yana tambayar ta. A firgicewa ta yi nan jikinta ya fara rawa kamar wacce aka jonawa lantarki, tsaki yai tare da barin ɗakin da sauri Maman su ta yi kanta ita da Zaliha suna taɓa ta hankali a tashe Maman su ta kwantar da ita tare da riƙe mata hannuwa dan har idanunta sun firfito tamkar wacce rai yake shirin barin gaggan jikinta domin har wani shiɗewa take tana jan numfashi, da ƙyar dai jikin ya daina rawa. A lura irin na Maman Nafisa Nuriyya ta kamu da cutar ɗimuwa wadda muddin aka yi mata magana me ƙarfi nan da nan take ficewa daga hayyacinta musamman ma idan namiji ne yai mata ihu abin na fin haka tsanani.

Alh. Aminu ne zaune gaban Hajiya Umma yana jin kalaman da take jero masa tare da miƙa masa hotuna murmushi kawai yai mata kana ya ce "Umma duk wannan hotunan basu yi mini kyau ba.."
"Daure dai ka duba dukkanin su kyawawa ne" Gyara zaman sa ya yi yana faɗin "Ita ma tana da

nata sihirtacciyar kyau ɗin, doguwa ce me dirarriyar jiki, tana da nutsuwa yanayinta ba mace ba ce me son hayaniya, zagayyen dogon fuskanta yana ɗauke da hanci zar idanuwanta irin shanyayyun nan ne wadda da zaran ta kalle ka za ka ji wani yanayi, a gefen kuncinta na dama tana ɗauke da dimful bakinta ɗan daidai tana da tsayi sai ita ba fara ba ce yanayinta mace ce me sanyi domin ko tafiyarta a sanyaye take yin sa.." Dakatar da shi Hajiyarsa ta yi tana jinjina irin wannan soyayyar da yake yi wa yarinyar da har yau bai san sunan ta ba.
"Kenan ka ƙare mata kallo? Ka san dai irin wannan kallon babu kyau.."
"Ba haka ba ne Umma ni kaina ban san lokacin da na yi hakan ba.." Miƙewa ta yi tana faɗin "An ɗauki tsawon watanni amma ba ka samo ta ba, na samo maka kyakkyawan yara amma kaƙi amincewa da su lallai sai ita bayan har yau ba ka san inda take ba.."
"Allah zai bayyana min ita" Juyowa ta yi ta kalle shi na 'yan daƙiƙu kana ta ce "Zan je gidan Zuwaira domin tun jiya take kira akan za mu yi magana idan za ka fita ka ce da Hannatu ('yar aiki) ta samu Habu drive su je kasuwa." Miƙewa yai yana faɗin "Muje sai na ajiye ki ni ma zan bi ta wajen Sa'id" Tare suka jiro suna hira gwanin sha'awa shi ya buɗe mata motar ta shiga kana shi ma ya shiga "Umma zan dawo da Suhaima domin banga alfanun zaman ta a can ba Laraba ma ta mayar da hankalinta kan kasuwancin ta na tura ta akan su haɗu da Amratullah su dinga gudanar da al'amuran karatu tare amma taƙi yarda wai can akwai takura bata iya barcin asuba sai a dameta da karatu gabaɗaya Laraba ta ɓata min yara da ɗabi'ar banza ban isa na yi magana a yi min abin da na ce ba, gwara ta dawo nan ɗin zan fi samun nutsuwa domin bazan mata abin da take so ba, shi ma Hisham ɗin ba yadda na iya ne shi ya sa ta ɗauke shi daga nan ita kuma mace ce ba zan iya ɗaukar ta zuwa wata duniya karatu ba" Yanayin da yake maganar zai bayya maka ran shi ya sosu da abin da matarsa take masa.
"Gaskiya ko ni ban goyi bayan a ɗauki ɗiya mace zuwa wata ƙasa karatu ba, Allah ya kyauta ya kare mana zuri'a"
Har gidan ya kai ta kana ya nufi inda Amininsa yake. Da ke tana son ta yi tattaki shi ya sa lokacin da ta fito daga gidan 'yar'uwar tata ba ta kira shi ba daidai zata sha kwana ta ga dandazon mutane tana muhawara Daga ƙarshe abin sai ya koma kamar faɗa mamaki ta ji ganin yadda manyan mutane suke ƙoƙarin ba hammata iska. "Assalamu alaikum!" Dudum! Babu wadda ya juyo ba re ta sa ran za a amsa mata cikin ɓacin rai ta fara magana "Haba bayin Allah sai ka ce ba musulmai ba, a yi Sallama ba za ku amsa ba ko dai tunanin nawa ne bai ba ni daidai ba?" Juyowa suka yi suna shirin surfe ta sai dai ƙwarjinta da yadda ta yi shigar kamala ne ya sa su dakatawa ɗaya daga cikin su ya amsa mata da faɗin "Barkanmu dai Hajiya" Hajiya Umma ta ce "Me ke faruwa a nan naga kun tsaya kun yi cirko-cirko.." Kan ta ƙarasa maganar ɗaya daga cikinsu yai caraf yana faɗin "Wannan la'anannen ne yai min alƙawari ya saɓa..." Da sauri ta dakatar da shi tana faɗin "Yaa Subhanallah! Haba bawan Allah a dinga tauna magana kafin a furzar sam wannan kalamin bai da ce ya fito daga bakin muslmin ƙwarai ba, ka yi magana kai tsaye ban da zagi da cin zarafi" Tsaki yai yana faɗin "Hajiya wannan mutumin ya cancanci fiyye ma da haka, nan muka yi da shi akan zai ba ni auren babbar ɗiyarsa dan ita ce me nutuwar dubu talatin ya karɓe min yanzu ina cewa ya ba ni kuɗi yana kawomin wani ƙaulin da ban san da shi ba"
"Ya batun auren fa?" Ta tambaye shi tana kallon Hamisu Saleh Baban su Nuriyya juyowa yai domin tun da aka fara maganar be ce musu ƙala ba, "Cewa yai wai ya fasa aure ni kuma yanzu ba ni da kuɗin da zan biya shi, ina ta ba shi haƙuri ya ƙi ya,  gwara dai ya karɓeta a hakan in

kuma ya ƙi wlh kuɗin sa ba labari" Gyaɗa kai ta yi tana faɗin "Kai don me ya sa ba za ka auri yarinyar ba yanzu?" Tsaki mutumin yai kana ya ce "Gwanjo ce fa, yarinyar da maza ba ɗaya ba har uku suka dinga hawa da sauka shi ne zan ɗauka..." Runtsa ido ta yi tare da ɗaga mishi hannu alamar ya isa, ɗaya daga cikinsu ne ya ce "Haba! Wannan fa ƙaddara ce don me ya sa ba za ka karɓe ta ka rufa mata asiri ba? Idan ba ka son auren ta me ye na buɗe maganar? Wannan ai tozarci ne, duk cikin mun nan muna da 'ya'ya babu wadda ya wuce ƙaddara" Daga nan ya fayyace mata duk abin da ya faru da Nuriyya saboda tsananin tausayi sai da ta zub da ƙwalla tana Allah wadai ga duk wadda yai mata haka. Jakarta ta buɗe tare da ɗauko bandir ɗin 'yan ɗari biyar-biyar ta wurgawa mutumin kana ta kalli Baban su Nuriyya tana faɗin "A ɗaura auren da ɗana ga sadaki" Bandir ɗin 'ya dubu-dubu guda biyu ta direwa Baban Nuriyya 200k jiki na ɓari ya kwashe kuɗin yana faɗin "To madalla lallai Nuratu an yi goshi.." Dakatar da shi Harisu yai yana faɗin "Hajiya kin san kuwa idan kika ƙoƙarin dasa iri? Wannan fa ba mutumin arziki ba ne da za ki dasa iri har ta yi yabanya.." Cikin ɓacin rai Baban su Nuriyya ya daka mishi tsawa yana faɗin "Harisu fita idona na rufe! Tun da an biya ka ka yi wucewar ka, kuma ka kwana da sanin za ka dawo da sauran dubu ashirin domin wallahi ba za ka ci su ba" Jijjina kai kawai Hajiya Umma take yi tana tur da hali irin na Baban su Nuriyya, Malam Sule wanda yai mata bayani shi ya tsaya matsayin wakili ga Aminu shi kuwa Baban su Nuriyya daga cikin waɗanda suke buga caca ne ya zaƙulo ɗaya ya zama wakili Nuratu nan aka bayar sannan aka amsa daga ƙarshe jama'a suka shaida ɗaurin auren Aminu da Nuriyya daga nan Umma ta ba shi adireshin ta tare da sanar da shi cewa zata turo ɗan nata domin su gana da Nuriyya batun tarewa kuwa ba yanzun ba su dakata tukun. Washe baki kawai yai yana gyada mata kai tare da faɗin. "Ai babu komai Hajiya duk lokacin da kuke da buƙatar ɗaukar ta ƙofa a buɗe yake ni dai sisi na ba zai shiga hidimar tariyar ta ba, ku da kuka ga za ku iya, ku za ku yi kome" Hajiya Umma ta ce "Ai da ma bamu buƙatar komai naku, Allah dai ya sa ka gane wannan ba ɗabi'ar mutan ƙwarai ba ne" Daga haka ta nufi gida.

** ** * ** ***

Kallon Aminin nasa ya sake yi yana faɗin "Wai da gaske ka samo ta?" Murmushi yai yana faɗin "Ƙwarai kuwa, cikin tarkacen hotunan Amrah na islamiyya na ganta da na tambayi Amrah sai ta ce min ai ƙawarta ce ajinsu ɗaya, nan ta shiga ba ni labarin yarinyar da yadda mahaifiyarsu take ta faɗi-tashi gurin inganta rayuwarsu.." Cikin zumuɗi ya katse shi ta hanyar faɗin "Muje ni ka kaini.." Wayarshi ne ya katse masa sauran maganar ta sa ganin Hajiyarsa ce me kiran ya sa shi ɗagawa cikin hanzari domin ba ya wasa da duk abun da ya shafi Hajiyar sa. Da sallama ya ɗaga wayar daga can ɓangaren Hajiyar ta amsa kana ta ce "Ina son magana da kai urgent!" Miƙewa tsaye yai yana faɗin "Ga ni zuwa" Daga haka ya sauke wayar yana faɗin "Muje gidan Hajiya daga nan sai in sanar mata" Mota suka shiga sannan suka nufi gidan. Shuru ya yi yana sauraron abin da take cewa har ta dire aya bai katse ta ba, illa gumin da ya haɗa kamar wanda ya haɗiye kunama. "Aminu ina ta magana ni ɗaya ba tare da ka ce komai ba?" Maganar ta ne ya dawo da shi daga duniyar tunanin da ya faɗa "To..t..o. ai Hajiya ban san me zance ba ne.." Dakatar da shi ta yi ta hanyar faɗin "Ba ka san me za ka ce ba?"
"Hajiya Aure fa kika ce kin yi mini haba! Sai ka ce yaro ƙarami.."
"Ungo nan gidan ku na ce, ka ji ɗan ƙaniya ko"
Hon. Sa'id ya ce "Yi haƙuri Umma duk ba abin ba na faɗa ba ne kai Aminu ka faɗa mata

maganar.." Dakatar da shi tai cikin ɓacin rai "Wata magana?" Kallon Aminin na sa yai domin gabaɗaya zancen  ya ruɗa shi. Gyaɗa masa kai Hon Sa'id yai alamar ya sanar da ita. "Hajiya da ma akan maganar yarinyar can ne mun samo inda take.."
"Ai ho! Yanzu na fahimta, to in ban da abin ka Aminu ai lokaci ya ƙure..." A rikice ya cire hular da ke kan shi yana faɗin "Innalillahi wainna ilaihir rajiun! Dan Allah Hajiya ki yi haƙuri.."
"Ban son jayayya Aminu batun ka gano inda take bai taso ba, ni dai na gama magana ka je ka samu wannan matar ku daidaita"

*Wannan littafin na kuɗi ne domin kasancewa cikin group za a tura ₦500 ta wannan account 2389596965 Aisha jubreel Zenithbank Sai a tura shedar biya ga wannan Number 09079740079 please idan ba saya za ki yi ba karki ɓata lokaci wurin yi min magana.*

#Amnoor
#Sadstory
#Destiny
#Hotlove
#Romance
[5/9, 11:43 PM] FARHATULKALB💔🤗: *_♡AMNOOR...!_*
_A Romantic Story_

®
FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION📚
★F. W. A★

Free page 19_20

*H-P Place Group*

Riƙo shi Hon. Yai tare da faɗin "Haba da Allah! So kake ka illata kan ka ne ko yaya? Saura kaɗan fa ka buge da ƙofar nan.." Leƙowa Umma ta yi tana faɗin "Me nake ji haka? Aminun ne yake ƙoƙarin kassara kan shi don na ce ya je su gana da matarshi?" Runtsa ido yai da ƙarfi domin kalmar *MATA* tamkar saukar mashi haka yake jin abin a zuciyarshi. Haka suka fito haraban gidan motarshi yake ƙoƙarin shiga cikin ƙarfin hali domin gabaɗaya gwiwowinsa sun sace tamkar tayar mota "Dan Allah ka yi min jagora zuwa inda take wallahi zuciyata na mararin son ganin t..." Dakatar da shi Umma ta yi ta hanyar faɗin "A kul! Karka kuskura bare har ka fara wannan gangancin domin wlh muddin na ji ka je inda yarinyar take wallahi zan saɓa maka.." Dafe kan shi da ke tsananin sarawa yai tuni ya riƙe saitin zuciyarshi da ɗayar hannun "Dan Allah Umma ki yi haƙuri wannan hukuncin yai tsanani da yawa a yi mana uzuri kin san lokacin ɗaya ba zai karɓi wannan lamarin ba, a yanzu yana da damar da zai kawo na shi zaɓin dan Allah Umma ki sassauta masa.."
"Duk wannan daɗin bakin naka Sa'idu ba ɗauka zan yi ba, ka sake jaddada mishi aure ne dai an riga da an ɗaura kuma wallahi na ji wani abu bayan wadda na ce zuciyoyi zai ɓaci"
Buɗe idanunsa da suka fara sauyawa saboda tashin hankali yai a hankali kamar me koyon

magana ya ce "An ya ba sauya min Umma aka yi ba? Mahaifiyata ba haka take ba, Umma bata taɓa yanke min hukunci me tsauri har haka ba ya zan yi da raina? Ya zan yi da tarin soyayyarta da ke nuƙurƙusan zuciyata wallahi akullu yaumi da ita nake kwana nake tashi ta yaya zan iya rabuwa da mace mafi daraja kuma mafi soyuwa a gareni farat ɗaya haka?" Ya ƙarasa maganar da ƙyar yana me ƙurawa Aminin nasa idanu.
"Aminu ka yi biyayya ga umurnin Umma Please ka sassauta wannan soyayyar duk fa wannan hidimar da kake ita fa yarinyar bata san kana yi ba, tana can tana rayuwarta cikin farinciki kai kuma kana ƙoƙarin jayya da Umma"
"To ya zan yi?" Hon. Sa'id Ya ce "Haƙuri domin ita ce komai muddin kuma aka ambaci wannan kalmar to tabbas an cuci wadda ake so ya yi ta" Lumshe ido yai tare da faɗin "Shi ke nan!" Duk yadda Hon. Sa'id Yaso fahimtar da shi amma ina karshe ma share shi yai, motar shi a gidan Umma suka bar shi domin yanayin da yake ciki ba zai iya tuƙawa ba.

Kallon shi Maman Nafisa ta yi ganin yadda yake washe haƙora yana ƙirga 'yan farare "Baban.." Be barta ta faɗi abin da take son faɗa ya katse ta "Alhamdulillah yau de buri na ya cika na aurar da wannan guzumar" Ya ƙarasa maganar tare da yin nuni da Nuriyya wacce take ta ƙoƙarin gyara kayan turaren da Maman su ta haɗa, wani irin ajiyan zuciya kawai ta sauke tare da zubewa a ƙasa da sauri Zaliha da ke shigowa tare da Manna su suka rufu a kanta "Ai ko mutuwa kike kina dawowa aure de ya ɗauru kuma gidan nera inda zan dinga samu ina da-na-sha Allah sarkin dadi!"
"Haba Baba! Me ya sa kake irin haka? Ka san de ba lafiya ne da ita ba har yanzu bata gama dawowa hayyacinta da har za a aza mata wani damuwa ba.." Tsawa ya daka mata tare za zare mata ido yana faɗin "Ke ma irin haka zan yi miki.." Turo baki Zaliha ta yi tana faɗin "Wallahi ba de ni ba, ai ko sama da ƙasa za su haɗe ba wanda ya isa yai min aure ba tare da wadda nake so ba"
"Ke Zaliha! Mahaifin naki kike faɗawa magana? Ban hane ku da irin wannan ɗabi'ar ba? Wallahi na sake jin irin haka zan fasa bakin nan"
"Banga laifinta ba, kinga de irin abin da nake gudu na haihuwar 'ya'ya mata ko? Yau wannan 'yar tayin ce take faɗa min magana? Ai ga irinta nan, kin je kin haifi yara basu san irin kalamin da za su dinga faɗawa manyansu su ba, se na karya ki wallahi in sake jin kin tsoma baki cikin magana ta" Turo baki tai gaba tana ƙunƙuni, tsaki ya ja sannan ya fita a ɗakin yana me faɗin "Aure de an ɗaura, kodayake sun ce ba yanzu za a yi tariya ba" Buɗe ido ta yi tare da fashewa da wani hargitsattsen kuka "Mama dan Allah me na yi wa Baba da ba ya ƙaunar ganin farincikina? Ni kenan daga wannan sai wannan, wallahi na gaji da rayuwar Allah ka ɗauki..." Rufe mata baki Maman Nafisa ta yi tana faɗin "Ki ce Alhamdulillah!" Da ƙyar ta iya furta kalman sannan ta koma jikinta ta lafe tana mayar da numfashi kiran Amrah ne ya shigo wayarta a hankali ta ja jiki daga na Mahaifiyarta sannan ta ɗauki wayar.

Bolingo Hotel.
Sautin kiɗe-kiɗe ne ke tashi a gurin yayin da 'yammata da samari suke casu tare da ɗaga kwalba ana ihu Suhaima na zaune tana danna waya gabanta kofi ne wanda yake ɗauke da ruwa kyakkyawan Guy ɗin da ke cashewa a fili ta ƙurawa ido ba ta ko ƙiftawa , Allah ya gani tana matuƙar son Dalil Amma sam ya ƙi ya kulata ta bishi har ta gaji, wannan ma ƙawarta Zee

ce ta ce ta zo yau yake Birthday party amma tun da ya masa gaisuwarta bai sake kallon inda take ba, ta lura da yadda yake ta duba agogo tare da kallon hanyar shigowa ga dukkan alamu wani yake jira wanin ma yana da matuƙar muhimmanci tunanin ta ya tsaya cak sakamakon ganin yadda ya tafi da sauri yana rumgume wata 'yar matsiyar da za su yi sa'a a shekaru. Ihu gurin ya ɗauka nan aka hau kiran sunanta kowa na ƙoƙarin gaisawa da ita. Na'ilah ce ta taɓa ta tare da faɗin "Fiddoh ki sake masa fuska mana Please bai kamata ki dinga sha mishi ƙamshi har haka ba" Ɗan murmushi ta yi tare da manna bakinta saman na shi wani irin deep kiss ta yi masa sannan ta kai bakinta saitin kunnen sa tana faɗin "Happy birthday Sweet Lil" Cikin murna ya riƙe hannunta har gurin da cake ɗin yake ya kaita sai murmushi yake zubawa domin bai tsmamaci zuwan nata ba, kasancewar ya daɗe sosai yana binta tana ƙin ba shi dama gashi cikin sauƙi ya samu ta sauko. Cake ɗin suka yanka shi ya fara sakawa a bakinta kallon ta yai tare da kashe mata ido duk yai kalan tausayi matsowa ta yi jikinshi sannan ta kai nata bakin saman na shi ɗif aka ɗauke wutar gurin zagaye hannayenshi yai a weast ɗinta tare manna ta sosai a ƙirjinshi yana amsar cake ɗin da take ba shi wani irin yanayi ta shiga dama ga shi kwana biyu bata ji sandar ya ratsa ta ba domin duk Guys ɗin da take da su basu mata irin yadda Ema yake mata. Cak ya ɗauketa tare da nufar haɗaɗɗen ɗakin da ya kama musu.
Kunna Flashlight ɗin wayarta Suhaima tai tana duba hanyar da suka bi roƙon ta Zee ta yi tana faɗin "Ki nutsu dan Allah.." Ƙwace hannunta ta yi tana faɗin "Karki sake min magana! Ta yaya zan nutsu bayan kina gani a gabana yake rawar jiki akan wannan figaggiya me kama da muciya sai ka ce Saude (Ta cikin Littafin Rubutacciyar ƙaddara) yarinya a bushe kamar ita ce wallahi se dai duk abinda zai faru ya daɗe bai faru ba, yau ko ni ko ita.." Bin bayanta Zee tai tana kiran sunan ta amma ko sauraron ta ba ta yi ba, kwalbar da ke kusa da case ɗin ta ɗauka nan take kuwa aka dawo da wuta ɗakunan da ke jere da juna ta fara bi tana neman inda suke.
Da ƙafarshi ya tura ƙofar kana ya nufi saman bed ya kwantar da ita zai ta shi ta jawo shi nan ya faɗo jikinta zuge zip ɗin wandon shi ta yi tare da fitowa da bananarshi a gefe guda kuwa tana kan bakin shi kamar mayyar da ta shekara bata samu nama ba, sosai take wasa da bananarshi tare da shafo saman shi lamarin da ya sa shi ɗauke wuta kenan.
Duk yadda ya so ta ƙyale shi ya cire kaya ƙin yarda ta yi domin a ganinta ɓata lokaci ne shi ma haka ya biye mata suka ci gaba, gefe tai da ɗan pant ɗin da ke jikinta wanda shi da babu duk ɗaya, a haka ya haye tare da dannan zandariyarshi zuwa tekun daɗi tare suka saka ihun daɗi, tamkar wanda ya sha ƙarfin doki haka ya dinga buga mata dama ya riga ya shirya ma zuwan nata sosai ta maƙale shi tana faɗin "Ohhh Ahahhhh Sweet Lil washhh fuck..." Da ire-iren kalman nan take sake ɗaga masa hankali wanda ya sa shi sake zage damtse yana buga mata wutsiya. Suna tsaka da jin daɗi suka ji an banko ƙofar da ƙarfi yana ƙoƙarin sauka ta riƙe shi gam domin dab take da zubar da ruwa "Ohhh My God! Sweet Lil wayyo Ashhhhh Hahhhh Ohhhhh!" Kunna wutar ɗakin ta yi nan haske ya gauraye ko'ina runtsa ido Suhaima ta yi tare da yin kukan kura ta afka kansu "Allah ya isa min Dalili! Da me wannan muciyar ta fini? Ka kalli yadda kake ride ɗinta kana kiran sweet...! Da aure nake son ka ba da ƙazamin rayuwa irin wannan ba, wallahi se na kashe ku zan kashe ki ƙaruwa ƙazama kariya.." Ɗauke ta Fiddoh ta yi da wani gigitaccen mari tare da faɗin "Akwai 'yar iska irin ki, ki ce kariya wacce take bin namijin da be son ta , ki tambaye shi na taɓa bin shi? Ga shi nan ai kullum bina yake kamar zai mai da ni ciki saboda tsananin so ko ba haka ba ne my sweet Lil?" Gyaɗa mata kai ya yi yana jin takaici katse masa jin daɗin da Suhaima ta yi, ƙofa ya nuna mata tare da faɗin "Fita a nan!" Kwalbar da ke

hannunta ta buga mishi tare da fashewa da kuka "Wallahi Lil Ina son ka! Amma gwara na kashe ka ita ma zan kashe ta, domin babu shegiyar da ta isa ta raɓi abin da nake so!" Kara Fiddoh ta yi da ƙarfi tare da ture Suhaima da ƙafa nan fa dambe ya barƙe cikin haka Fiddoh ta ɗauki fasasshen kwalban ita ma ta rotsa mata a goshi ihun su ne ya fargar da sauran jama'ar da gudu Zee ta ƙarasa shigowa ganin yadda jini ya ɓata gadon ne ya sa ita ma ta sa ihu tare da jin kan Suhaima tana jijjigata wacce tuni ta suma da gudu Na'ilah ta kama hannun Fiddoh tana janta akan su bar gurin sai dai kash! Suna fitowa sai ga 'yan sanda. Nan suka tasa ƙeyarsu Dalil da Suhaima direct aka yi asibiti da su da ke ciwon Suhaima bai shiga sosai kamar yadda ta fasa ƙeyar Dalil ba, ana gama wanke mata suka ta sa ƙeyart, kwana suka yi cikin fitsari da zarni ga cizon sauro zagi kan Fiddoh ta auna musu buhu-buhu domin sun hanata waya bare ta kira gida gashi sun hana kowa ganawa da ita Na'ilah sai sintiri take tana basu haƙuri, sai washegari aka ba su damar ganawa da mutane jiki na rawa Suhaima ta fara kiran Hajiya Larai, Sai dai wayar tata baya shiga ta yi tunanin kiran Daddyn su (Hon. Sa'id kasancewar haka suke kiran shi) sai aka yi rashin dace shi ma wayar ta sa ba ya shiga tana kuka haka ta kira Alh. Aminu tare da sanar da shi halin da take ciki.
Na'ilah na ƙoƙarin biyan kuɗi Fiddoh ta dakatar da ita domin ta ce wlh se dai Suhaima ce za ta biya domin ita ce silar zuwanta nan gurin ƙarshe kamar za su kashe kansu saboda hayaniya duk yadda Suhaima taso taka Fiddoh abin ya wuce tunaninta domin Firdausi irin fitinannun matan nan ne masu naciyar faɗa, ba ta jin haƙuri sai dai idan ta gaji tun kanta ta ƙyale zuwan su Alh. Aminu gurin ne ya sa ta yin shuru tare da ƙure shi da ido, Bestie wancan mutumin ya haɗu fa, wlh farat ɗaya zuciyata ta amshe shi, Black beauty ga sanyin nutsuwa takun sa gwanin burgewa sugar daddy idan ya same ni 'yar sweet 17, zan shagwaɓa shi da yawa.." Cike da baƙin cikin jin kalamanta Suhaima ta ce "Ahir ɗin ki, Karuwa! Gwanjo wacce maza suka gama shiga da fita a jikinta, Dad ɗina ya fi ƙarfin kariya ballagaza irin ki.." Wani irin murmushi Fiddoh ta yi tare da faɗin "Zan nuna miki halin Karuwa ke bari ma kiji wallahi se na auri Uban naki kuma dole ki kira ni Mom! Domin ya yi min irin mijin da nake so kuma dole na yi kishi da uwarki"
Wani irin mugun kallo Alh. Aminu yake bin Suhaima da shi kuɗi ya je biya ran shi a ɓace domin bayanin da 'yan sandan suka mishi game da abin da ta aikata. Juyowa yai tare da kife ta da mari ya riƙe kunnen ta yana magana cikin ɓacin rai dama kwana biyun nan ran shi a ɓace yake musamman ma da Hajiya Umma tai mishi iyaka da abar ƙaunarsa.
"Wato ke har kin yi ƙwarin da za ki yi faɗa akan ɗa namiji kina fashe-fashen kai ko Suhaima? Ban hanaki yawon dare ba? Kodayake ba laifin ki ba ne tun da kin samu ɗaurin gindi amma ba komai zan yi maganin abin"
"Hi! Yaa Laj! Ka biya kuɗin duka har nawa domin ɗiyarka ce ta sa aka kulle ni, and pls ka riƙe faɗar har ku ƙarasa gida in ya kama ma a yi mata shegen duka, domin bata jin magana" Kallon Firdausi yai tare da jan tsaki ya figi hannun Suhaima suka nufi gidan Hajiyar shi.

Ɗauke kai Maman Nafisa ta yi daga kallon Firdausi "Yanzu Mamanmu ko sannu ba za ki ce mini ba?" A fusace ta ɗago tana nuna ta da 'yar yatsa. "Na aike ki? Wallahi Firdausi fita idona na rufe in ba haka ba zan yi mugun saɓa miki" Watsar da hannu Fiddoh ta yi irin I don't care ɗin nan sannan ta juya tana jin jawabin da Zaliha take mata game da auren da Baban su yai wa Nuriyya "Jar uban can! Na rantse da Allah se ya sake wannan auren ko kuma na yi mishi kutumar.."
"Zo ki fice min a ɗaki!" Maman su ta faɗa tare da miƙewa tana neman abun da zata buge ta da

shi domin ta lura har yanzu bata dawo cikin hayyacinta ba. "Mamanmu Rass fa nake! Ban shawu ba wallahi maganar gaskiya wannan Guy ɗin ba ya kyautawa ta ya zai aurar da 'yar'uwata ba tare da ya nemi shawara ba, na rantse sena ɓata mishi rai..."
"Innalillahi wainna ilaihir rajiun! Baban ne Guy? Firdausi lallai kin rika Ubangiji ya shirya ki" Maman Nafisa ta faɗa kana ta nufi gurin kayan turaren ta. Kallon Nuriyya da ke zaune shuru tai kana ta ce "Karki wani damu tsaf zan sa shi ya warware wannan abin" Ta faɗa tana me kwanciya kusa da ita. "Ke! Humm! Ɗazun nan naga wani haɗaɗɗen sugar daddy yasin ya haɗu sosai, shirya muje shopping na siya miki riga ko kala biyu da hijjabi dan ba saka gyale kike ba" Da sauri Zaliha ta ce "Ayya! Ni kuma fa Aunty Fiddoh" Hararanta tai tana faɗin "Kema shirya sai muje"

Wannan Littafin na kuɗi ne domin kasancewa cikin group y ₦500. A tura ta wannan account ɗin. 2389596965 Aisha jubreel Zenithbank Sai a tura shedar biya ga wannan Number 09079740079

#Amnoor
#Sadstory
#Destiny
#Hotlove
#Romance
[5/9, 11:43 PM] FARHATULKALB💔🤗: *♡AMNOOR...!*
_A romantic story_

®
FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION📚
★F. W. A★

H-P Place Group.

Free page 21-22

A nutse ta matsa gefe inda babu hayaniya tare da manna wayar da kunnenta tana sake faɗin "Ki jira ni yanzun za mu dawo sai muyi maganar." Juyowan da za ta yi ne ta ga mutum tsaye yana ƙare mata kallo tunanin inda ta san shi take, zuwa can dai ganin taƙi yin magana ne ya sa shi faɗin Ashe dai ke ce, yau dai ba zan yi ƙuncin baki ba, ki faɗa min sunanki tare da na gidanku domin na ɗau tsawon watanni ina neman ki" Ɗagowa ta yi tare da watsa mishi narkakkun shanyayyun idanunta wanda yake ɗauke da zara-zaran gashi, cikin ƙwayar idon nata har wani maiƙo da sheƙi me fisgan hankali yake, shi bai taɓa lura da tsananin kyan nata ba sai yau da sauri ya ɗauke idonshi daga kallonta yana sakin ƙayataccen murmushin da ya ƙarawa kamilalliyar doguwar fuskarsa kyau da haiba. Waigowa yai yana sauraron zazzaƙan daddaɗan muryan da ke ratsa masarrafan da ke kai masa saƙo kai tsaye zuwa ga kunnensa.
"Sunana kuma? Me za ka yi da shi? Me sanin gidanmu zai amfane ka da shi?" Ta ƙarasa maganar muryanta na rawa saboda tsoro tare da kallon Zaliha da ke ƙoƙarin ƙarasowa wurin su. "Ki nutsu! Ba wani abu zan miki na cutarwa ba, da alkairi na zo auren ki zan yi..." Wani irin

duka ƙirjinta yai wadda ya sa har tana ƙoƙarin yin ƙwarewa sai dai shaƙuwa ne ya riƙe ta, da sauri Zaliha ta ƙaraso tare da riƙe ta suka bar wurin bin su kawai yai da ido yana mamakin yadda take a tsora ce, juyawa yai tare da shiga motar shi ya nufi gidan Hon. Sa'id domin yana son ganawa da Amrah.

A rikice suka ƙarasa gida domin yanayin da take ciki abun ya ta'azzara zaunar da ita Mamansu ta yi tana yi mata fifita tare da shafa mata kanta hankali a tashe domin yanayin yadda ciwon yake zuwa ma Nuriyya ba ƙaramin kiɗimasu yake yi ba. Kallon tuhuma ta yi musu rai a ɓace take faɗin "Me kuka mata? Shi ya sa wallahi ban so fitar nan naku ba, babu yadda zan yi ne kawai dan abu kaɗan yake birkitata.." Fiddoh ta ce "Ki yi haƙuri Mamanmu!"

Zaliha da ke zaune da hannu bibbiyu tai tagumi ta ce "Mamanmu to akai Aunty Nuriyya asibiti mana sai aji me ke jawo mata wannan yanayin ko Fiddoh?" Ta ƙarasa maganar tare da kallon Fiddoh "Bari dai Amrah ta dawo don yanzu ta fita wai Daddy na kiran ta" Suna zaune shuru har Babansu ya shigo yana baza ƙamshi zama yai gefen ta gaban goshin sa Fiddoh yana washe baki domin dama zero yake ya san zai samu wani abu wurinta "Fidausi ya aka yi naga duk kunyi kalan 'yan zaman makoki sai ka ce wadda aka ce na mutu"

Wani banzar kallo tai masa tana faɗin "Da a ce kai ne ka mutu yaushe za mu yi wannan zaman? Ai wallahi DJ zan ɗauko na yi ta tiƙar rawa ina dariya dan an rage mugun iri ne, Uban da be san ci 'ya'yansa ba balle akai ga karatu, tun da Mamarmu ta yi mana ƙoƙarin muka kammala sakandiri fa muke zaune, tun buɗewar idanuna ita ce ɗawainiyarmu ta yi ayyuka ƙarfi, wahala, ga azaban baƙaƙen magana daga bakin mutane, ga zafin rana, duk don saboda mu. Ta shiwar yayarmu ta ɗaura niyar taimaka maka sai dai kash! Wasu 'yan iska suka datse mana farinciki ba su duba rayuwa da yanayin da  muke ciki ba, suka take min 'yar'uwa wallahi ko ba jima ko ba daɗe akwai ranar ƙin dillancin duk ranar da na yi arangama da wa'yannan 'ya'yan Allah wadai ɗin hmm! Allah kaɗai ya san tanadin azaba da raɗaɗin da na yi musu.."

Dakatar da ita yai ta hanyar miƙa mata hannu bayan ya miƙe yana kallon jakarta, "Bani wani abu zan wuce ne"

Cike da shaƙiyanci ta ce "Mu je sai na ba ka.."

"Kinga bana son iya shege bani kawai na yi wucewa ta"

Ya faɗa tare da haɗe fuska. Tsaki Mamansu ta ja tare da miƙawa Nuriyya ruwa tana faɗin "Sallame shi dan Allah ya tafi tun da shi Allah ya yi shi mara lura bare ya fuskanci ya muke ciki.." Dubu ukun da take miƙa masa ya karɓa tare da tattara babbar rigarsa yai gaba.

"Ta yi aure fa kika ce Amratu? Wa ta aura? kuma a ina gidansu yarinyar yake? Ya sunan ta?" Kallon sa ta yi ganin yadda ya birkice tare da jero mata tambayoyi.  Alama mahaifinta yai mata a kan ta tafi miƙewa ta yi ita ma tana kallon yadda Daddyn Hisham ya birkice duk sai ta ji tausayin sa, domin ta lura ƙwarai yana son Noor ɗinta, musamman ma da Abbanta ya ba ta labarin yadda  suka haɗu, ta san da shi ya aureta za ta sha gata da soyayya sai dai momy larai fa za ta iya kashe musu 'yar mutane domin baƙin kishi ne da ita, sai kuma ga shi Allah ya yi mata gyaɗar dogo.

"Wai me ya sa kake katse ni a duk lokacin da nake gaf da cimma muradina ne kam?" Ya faɗa cikin yanayin damuwa tare da kallon Aminin nasa. "Gani nai kana ƙoƙarin ƙetare dokar Allah, ita fa yarinyar matar wanin ka ce, way not kai ma ka nutsu ka bi zaɓin mahaifiyarka, wata biyar fa ana abu ɗaya,  ka bar 'yar mutane da nauyin aure na farko ba sauke mata haƙƙinta ka yi ba, ta

ya za a takura yarinya bayan kuma tana da miji.." A harzuƙe ya kai mishi naushi, kaucewa Baban Amrah yai yana dariyar shaƙiyanci tare da faɗin "Haba mutumina cool down ka je ku daidaita da wannan amariyar anjima fa ba a haɗu ba, Larai ta nutsu tana harkan kasuwnacinta kai kuma ta barka da rumgumar filo tare da juyi cikin dare.." Miƙewa yai yana faɗin "Idan ka gama iskancin naka ni zan wuce gidan Umma" Dariya yai sannan shi ma ya miƙe yana faɗin "Ai tare za mu, domin ta ce mu je na san duk ba zai wuce maganar wannan auren ba"
Gaba yai yana jan tsaki domin har cikin ran shi ya tsani wannan maganar, matar ma baya buƙatar ganin ta.
Yana zaune tare da sauraron kukan da Suhaima take rero masa tana ba shi haƙuri a kan ya mayar da ita wurin momynta dan Umma aikin girki take saka ta ita kuma ba so take ba, ɗauke kanshi yai daga gare ta domin ba ya jin zai mayar da ita "Dan Allah Abba ka sa baki wallahi ba zan ƙara neman rigima ba" Murmushi Abban Amrah yai tare da kallon Aminin nasa. "Tun da ta yi nadama a ƙyale min ɗiya ta koma wurin gyatumarta.." Wani mugun kallon da Alh Aminu ya auna mata ne ya sa ta barin wurin cikin gaggawa tare da fashewa da kuka. Ga shi ko ta kira wayar momynta ba ya shiga kuma an hanata fita tana son zuwa duba jikin Lil amma Umma ta yi mata iyaka da ƙofar falo balle akai ga bakin get.
Gyaran murna Hajiya Umma ta yi ta shiga musu faɗa ta inda take hawa ba ta nan take sauka ba, ganin yadda Alh. Aminu ya watsar da maganar auren an shafe watanni a gefe guda kuma gantalin da Laraba take na yawon garuruwa da sunan kasuwanci ba ƙaramin ƙona zuciyarta yake ba, domin dai ta tabbata har yanzu bata ɗauki Aminu da wani muhimmanci ba,
"Wallahi wannan zaman da za mu yi ya zama na ƙarshe ka tafi gidan su yarinyar nan ku daidaita kanku dan a satin nan zata tare ba wani magana ɓata lokaci tunda abu na tafiya shekara" Ɗagowa yai tare da gyaɗa mata kai yana faɗin "In Sha Allahu za a yi yadda kika ce" Da mamakin kalamansa ta sake kallon shi ganin yanda ya sauko babu jayayya kamar lokacin baya, "Yawwa Madalla Ubangiji yai maka albarka Aminu na" Murmushin yaƙe yai mata sannan ya fara laluben makullin motarshi tare da ficewa a falon ya barta suna tattaunawa da Abban Amrah nan ta sanar da shi inda gidan su Nuriyya yake da kuma yadda take so a yi komai ba tare da Labara ta sani ba sun tattauna sosai inda ya tsayar da maganar da cewar zai gyara part ɗin Amrah domin yarinyar ta zauna a can na ɗan lokaci. Yana fitowa ya shiga mota tare da kallon Aminin nasa ya ce "Na ji daɗin yadda ka amince mata ba tare da jayayya ba, yanzun muje gidan su yarinyar" Shuru kawai yai masa har suka ƙarasa anguwar tsayar da motar yai yana ƙarewa gidan da suke fuskanta kallo. Dama tun fitar su Umma ta kira Baban su ta sheda mishi za su zo, yana ganin tsayuwar motar ya ƙaraso kallon up and down Baban Amrah yai masa ganin yadda yake taku ɗaɗɗaya yana maza gare.
"Barka da zuwa Alh" Ya faɗa tare da miƙa masa hannu nan shima ya miƙa masa suka yi musabaha sannan ya gabatar musu da kanshi tare da musu iso zuwa ɗakin shi da ke wajen gidan. Ɗakin fess yake kasancewar shi mutum ne me tsafta ɗan ƙwalisa domin ya ƙawata ɗakin da kayan ƙyale-ƙyale na zamani cike da shaƙiyanci yake magana tare da gabatar musu da kayan motsa baki kana ya ce "Har yanzu ban gane wane ne angon ba" Kallon Alh Aminu da ke ta murmushi yaƙe Baban Amrah yai kana yai masa nuni da cewar "Ga shi nan" Sunkuyar da kai Alh Aminu yai ganin yadda Baban su yake ƙare mishi kallo yana gyaɗa kai. "Madalla bari na turo muku ita" Yana fita Baban Amrah ya ce "Amma da ganin wannan sirikin naka ɗan duniya ne" Shi dai bai ce masa komai ba. Lokacin da Babban su Nuriyya ya shigo ya yi daidai da zura

ƙatuwar hijjabinta tana ƙoƙarin yin Sallar la'asar da ya wuce ta domin yau da zazzaɓi ya wuni, "Nuratu ki shirya kina da baƙi a ɗaki na, ki yi sauri domin ba jimawa za su yi ba"
"Ai ka bari ta yi Sallah ko kuwa?" Maman Nafisa ta faɗa tana hararar shi. Jiki a sanyaye ta yi Sallar tana sallamewa ya azal-zala musu wuta ta yi ta fito Fiddoh da fitowarta kenan daga banɗaki ta kalle shi tare da faɗin "Ai ta amsa za ta zo, ka je mana, ka tsaya kana surfawa mutane ruwan bala'i haka za ta je ba tare da ta shirya ba?" Fita yai yana masifa. "Dalla ke ma ki shirya kin yi tsaye se rawar jiki kike ba dole a cika mutane da surutu ba" Fashewa kawai Nuriyya tai da kuka domin ta rasa ya ma za ta yi. Ɗauke kai Maman Nafisa tai domin wannan ba maganar da za ta saka musu baki ba ne. "To ni me zan yi? Dan Allah shirya mu je tare.." Zaro mata ido Fiddoh ta yi tana faɗin "Wa? Taɓɗi! Ai ki shirya kawai ki je wurin mijinki ba inda za ni"
Juyowa ta yi tana kallon Mamansu da ke zuba turare a kwalba, "Ayya Mamanmu dan Allah ki ce mata muje tare" Ba tare da ta ɗago kanta daga abinda take yi ba ta ce "Ku je tare da Zaliha" Zaliha da ke taya ta zuba turaren ta zunɓuro baki tana mita ita tana aiki za a ɗaga ta. "Ai ko na je wallahi ba zama zan yi wurin mata da miji ba" Ta faɗa tana share hannunta a jikin hijjabin da za ta saka, kallon yadda Nuriyya ke shirin fita ba tare da ta shafa mai ko turare ba "Eyye! Dama haka ake zuwa wurin miji bagajan-bagajan ba shafa mai bare hoda ko turare? Kuma da wannan uban hijjabin za ki tafi sai ka ce matar malam?" Dakatawa Nuriyya ta yi tare da juyowa tana kallon yanda take hijjabin da take Sallah ne, ba shi da wani ainu. Bata aune ba ta ji Fiddoh ta buɗe turare tana zuba mata. Cikin faɗa Maman su ta ce "Wai Firdausi lafiyar ki ? Turaren nan fa an riga da an biya na gama musu haɗin kayan amare ne fa.."
"To ai ita ma amariyar ce" Fiddoh ta faɗa tana dariya tare da kallon yanda Mamansu ta haɗe fuska "Yi haƙuri Mamanmu ni zan biya sai a musu wani shi ke nan? Ku kuma tsayuwar me kuke? Ko se Baba ya dawo ne za ku tafi?" Hannun Zaliha ta riƙe suka fita Zalihar ce ta yi Sallama sai da aka amsa musu sannan suka shiga.
Zama suka yi kan ledar da ke malale ƙasan ɗakin cike da ladabi Zaliha ta gaishe su da murmushi suka amsa domin yabawa da nutsuwa tare da tarbiyyanta abin ya burgesu ƙwarai. Nuriyya kam har yanzun kanta na ƙasa da murmushi Baban Amrah ya kalli Nuriyya tare da taɓa Aminin nasa nan shima ya ɗago yana duban inda take, mutuwar zaune yai yana sake kallonta "Ita ce fa!" Ya faɗa yana kallon Baban Amrah wanda ya miƙe tare da yafito Zaliha suka fto tare da nufar wurin mota yana tambayarta sunan ta.
"Suna na Zaliha Hamisu Saleh"
"Ni ce name amma kina mace na ji ki da turaren maza kuma haɗi na musamman" Turo baki ta yi tana faɗin "To ba aiki ɗurawa nake yi ba, shi ne Mamanmu ta ce se na rako Aunty Nuriyya" Dariya domin yanayin da yarinyar take magana ya burge shi sosai haka suka ci gaba da hira tana zuba mishi surutu da shirme shi kuwa yana biye mata can dai ya tambaye ta game da karatu shuru ta yi masa ba tare da ta ba shi amsar ba.
"Turaren na siyarwa kuke yi?"
"Eh kuma harda haɗin amare Mamanmu ta iya da na maza ma duka ana yi"
"Je ki kawo min su na gani" Da gudu ta shiga gida ta ɗauko mishi kwandon da take zuwa talla da shi.
"Lallai Mamanmu ta iya turare masu kyau zan so mu yi magana da ita domin haɗin ya yi min kyau, kodayake zan turo Amrah sai su yi magana.."

"Amrah? Aunty Amrah dai da na sani ƙawar Auntyna?"
Murmushi yai mata gwalo ido ta yi tana faɗin "Taɓ! Abun da mamaki wallahi to shi wancan mijin Aunty na ya alaƙarku yake da shi?"
"Alh Aminu shi ɗin Amini na ne tun yarinta komai namu tare muke yin sa" Daga haka hira ya ɓarke tsakaninsu Zaliha nata zuba mishi shirme yana murmushi.

"Bisimillah ta so ki zauna a nan" Ya faɗa tare da nuna mata gefen sa. Girgiza kai ta yi tare da ƙara takurewa da ƙyar ta iya buɗe baki ta ce "Ina yini.."
Maƙalewa sauran maganar tata yai jin ya zauna gab da ita, ɗagowa ta yi da sauri tare da watsa mishi Lulu Eyes ɗinta da ya tara ruwa, murmushi ya sakar mata tare da riƙe fuskarsa da hannun biyu yana kallon kyakkyawan siririn fuskanta. "Kina mamaki ko? A baya na sha neman ki kamar zan yi hauka, domin an ƙidaya min lokaci na fito da matar aure har wa'adi ya cika ba tare da na ganki ba, lokacin da muka haɗu sai na ga gabaɗaya tsoro ne ke ɗawainiya da ke, da na tuntuɓi ɗiyata 'yar wajen Aminina Amratullah ita take sheɗamin cewar ke matar aure ce domin an ɗaura miki aure watanni baya, na ji babu daɗi nan na yanke shawarar zan amshi zaɓin da mahaifiyata ta yi mini sai gashi a she ke ce, ina ta cika ki da surutu ba tare da na sanar da ke waye ni ba. Sunana Alh Aminu ni haifaffen nan garin Abuja ne, ina da mata ɗaya wacce ta kasance 'yar'uwata ce, yaranmu biyu Hisham shi ne Babba wanda a yanzu yana ci gaba da karatunsa a ƙasar waje, se Suhaima. Matata tana matuƙar so na kuma tana da kishi sosai bana wasa da duk wani abun da ya shafi iyalina musamman Ummata ina son su.
Ni ɗan kasuwane ina ƙasuwanci har ƙasashen ƙetare, anan ina da shagunan sarƙoƙi, ni kaɗai nake ta magana ba tare da kin ce min komai ba"
Ɗan matsawa ta yi ganin yadda suke gab da juna, sake ƙanƙame jikinta take yi domin gabaɗaya a takure take "Babu abinda zan yi miki" Ya faɗa tare da matsowa ya kamo hannunta ƙara ta saka tana ƙoƙarin fisgewa nan da nan ta shiga rawar jiki  "Subhanallahi!" Ya faɗa tare da riƙe ta sosai a jikinshi yana mamakin wannan lamarin nata. Wayarshi ya ɗauka tare da kiran Baban Amrah yana faɗin ya tura mishi Zaliha. Kallon Zalihar yai tare da faɗin "Har ka gama shan love ɗin ne da wuri haka?" Tsaki Alh Aminu yai tare da kashe wayar sannan ya ɗauketa ya ɗorata akan kujera kana ya zauna kusa da ita.
Kuɗi masu yawa Baban Amrah ya miƙa mata tare da faɗin "Ki bawa Auntyn ki, domin zuwan gaggawa ne bamu samu munyi tsaraba ba" Maƙe kafaɗa ta yi tare da ƙin karɓa "Wallahi idan na amsa duka Mamanmu za ta yi min" Cike da yabawa da tarbiyyanta ya ce "Idan kika ce mata mijin Auntyn ki ne ba za ta yi komai ba, in kuma taƙi ki ajiye min" Da ƙyar dai ta amshi kuɗin sannan ta nufi ɗakin.
Kallonta yai tare da faɗin "Zan tafi amma zan dawo dole zan kaiki asibiti domin a duba lafiyar ki, ki kula da kanki" Ya faɗa tare da kai bakin shi goshinta yai mata kiss yana gyara gaban rigar tasa. Shigowar Zaliha ya ba shi damar fita kanta har yanzun a sunkuye yake sai da ya kusan fita sannan ya juyo ya yi daidai da ɗagowar da ta yi, nan idanunsu ya faɗa cikin na juna, da sauri ta ɗauke kanta daga kallon shi sannan ta miƙe ita ma jiki a sanyaye ba ta san ya ajiye mata kuɗi ba sai da taga Zaliha ta ɗauko tana miƙa mata. "Laa Aunty ga kuɗin ki manta da su"
Juyowa ta yi tare da kallon kuɗin wanda ya kusan talatin. Haka suka shigo cikin gida nan Maman su ta dinga faɗa ganin kuɗi har dubu hamsin "Mamanmu wallahi ban san ya aje min kuɗin ba.."

"Ke ba ni kuɗin tun da ba ta so.." Baban su ya faɗa tare da kai hannu zai amshe, da sauri Zaliha ta faɗa kan Maman su tana faɗin "Wallahi ba zan bayar ba, ai ina kallo Baban Amrah ya ba ka kaima" Fita yai a ɗaki yana faɗin yara duk babu me tarbiyya da zai dinga faɗar magana cikin ladabi da biyayya.

"Ji nai kana ƙamshi da alama dai sai da ka angwance.." Taka burki yai da ƙarfi yana kallon shi tare da faɗin "Allah zanci abu kazan ka.. Haba! Duk ka isheni da surutu da ke ni na rako jaraba duniya dole daga zuwa na hmm" Sai kuma yai shuru domin idan ya biye masa haka zai yi ta zolayar tasa a haka suka nufi gidan Aminu suna tattauna yanda tariyar zai kasance anan ne yake sanar mishi halin da take ciki wanda ya rasa gane mene ne, sun tsayar da maganar akan zai samu Amrah su tattauna yayin da Hon. Sa'id ya ce ya sanar da Larai halin da ake ciki.
A gefen guda kuwa ɗaya daga cikin 'yan group ɗin su ne ta samu labarin Alh Aminu ya yi aure ba tare da sanin matarshi ba nan fa aka kafa mitin tare da laluɓo number Hajiya Larai wacce take can Legas tana duba shagon kayan ta Fiddoh ce ta yi kiran a ɗaya daga cikin wayar da suke amfani da shi. Ganin baƙuwar number ya sa ta ɗauka tare da kara wayar a kunnenta tana faɗin "Hello!" Daga ɓangaren Fiddoh ta ce "Ki duba mun tura miki account ɗin mu ki turo da miliyan ɗaya mu kuma za mu faɗa miki abinda ke shirin faruwa daga ɓangaren mijinki" Tana gama faɗar haka ta kashe wayar jiki na rawa ta tura musu kuɗin murmushi Fiddoh ta yi tare da miƙawa Na'ilah wayar don ita ta gama aikin ta. "Ki yi gaggawar barin Legas ki dawo gida domin mijinki na shirin angwancewa domin tuni an ɗaura aure" Tana kawowa nan a zancen nata ta datse wayar tare da kashewa bayan ta ajiye layin a ƙasa. Zubur Hajiya Larai ta miƙe tana faɗin "Jar uban can! Ni ce za a yi wa kishiya? Duk yaushe aka yi wannan ban sani ba?" Jiki na rawa ta ɗauki waya tare da kiran layin shi sai dai baya shiga, haka ta siyi tikiti ba shiri ta kamo hanyar Abuja.

***
Yana ɗaya daga cikin ɗalibai masu hazaƙa da malaman ke ji da shi, nutsuwa haɗe da tarbiyya gami da biyayyarsa ne ya ƙara mishi ɗaukaka da farin jini, duk inda ya gifta nuna shi ake tare da yabon ƙwazo da hazaƙar sa. Mata da yawa suna bin sa daga fararen fata zuwa ga 'yan'uwansa 'yan Nigeria da suke tare a wurin sai dai ko ɗaga kai ba ya yi balle ya kulasu. Mace ɗaya ce ta tsaya masa wacce a kullum cikin mafarkinta yake kuma kullum cikin da-na-sani abin da ya aikata mata yake, kusan kullum suna waya da abokansa wanda su ma tun faruwar lamarin iyayensu suka ɗaga su a ƙasar kasancewar ta'asar da suke yi wa 'ya'yan mutane sai gaba yake yi, duk da haka ba su daina ba, domin sex ya zame musu tamkar ruwan shan su wadda in har ba su sha shi ba ba su jin daɗi iskancin na su ya shahara ne ya yi da suka samu gurbin karatu a jami'ar London inda suka haɗu da gogaggun tatattun 'yan iska wanda suka yi ƙaurin suna a harkan 'SEX GAME' idanunsu ya Buɗe fiyye da baya dan suna iya kwanciya da mace fiye da ɗaya a lokaci ɗaya duk da haka ma maneji suke yi dan har yanzu ba su samu mace kamar yarinyar can ba. Juyi yai a gadon da yake tare da runtsa idanunshi hoton abinda ya faru yana sake dawo masa tamkar yanzu aka yi sa ihu da magiyar da take mishi ne ya sake cika dodon kunnen shi.

Saura ƙiris free page zai ƙare.

Wannan Littafin na kuɗi ne domin kasancewa cikin group za a tura ₦500 ta wannan account ɗin 2389596965 Aisha jubreel Zenithbank. Sai a tura shedar biya ga wannan Number 09079740079

#Amnoor
#Sadstory
#Destiny
#Hotlove
#Romance
[5/9, 11:43 PM] FARHATULKALB💔🤗: *♡AMNOOR...!*
_A romantic story_

®
FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION📚
★F. W. A★

H-P Place Group.

Free page 23_24

Kuje ku yi Subscriber Channel ɗi na a YouTube. FARIN JINI HAUSA TV. Domin sauraron ƙyatattun littafanmu.

*Following me on Wattpad: ayshajb*
*Arewabooks: ayshajb*

Kuje Arewabooks za ku samu littafaina a can.

A kasalance ya sake buɗe idanun nasa wanda ya fara sauya launi saboda yanayin da yake ciki, wayarshi ya laluɓo tare da kiran Hajiya Larai wacce take ƙoƙarin saukowa daga matakalan jirgi ƙarar wayar tata ba ƙaramin kiɗimata ya yi ba, nan take zuciyarta ya fara dukan tara-tara buɗe jakarta ta yi sannan ta ɗauko wayar hannunta na rawa a hankali kuma ta sauke gwauron numfashi ganin Hisham ne me kiran nata zama ta yi a kujeran da ke kusa da ita kana ta kara wayar a kunnenta ba tare da ta ce masa komai ba, dan ta san maganar tasa ba zai wuce wannan yarinyar da suka hake mata ba, ita ta rasa wane irin masifa ne yake bibiyarta ɗanta yana neman haukacewa a kan yarinyar da bata san wace ce ba, shi ma kanshi bai san wace ce ita ba, amma duk ya damu a kan lallai sai ta binciko mishi ita, bari yau za ta yi maganin abun.
"Barka da warhaka Mome ya gida da su Hajiya?" Amsa mishi ta yi da faɗin "Kowa lafiya ya karantun naka ina fatan kana mayar da hankali?" Tamkar yana gabanta ya gyaɗa mata kai kafin ya ce "Mome wai har yanzu ba a samo inda yarinyar nan take ba ne.." Miƙewa ta yi daga zaunen da take ganin drive ya ƙaraso tare da faɗin "Zan ci mutuncin ka muddin ka sake min wannan maganar! Hisham ka fita idona na rufe daga kai har uban nan naka kun saka ni gaba

da fitina to wallahi ba za ku kashe ni da raina ba karka sake kirana muddin wannan maganar za ka yi mun" Tana kawowa nan ta kashe wayar tana jan tsaki tare da da ka ma driven tsawa "Dalla taka mota mu tafi ka wani tsare ni da ƙananun idanu kaman fincen ƙuma!" A gefen Hisham kuwa bin wayar ya yi da ido yana jin wani abu ya tokare masa ƙahon zuciyarsa.

Hamdala ta yi a ranta ganin motar tasa a gida da sauri ta fito ta nufi cikin gidan a falo ta jefar da jakarta kana ta nufi ɗakin sa. Daidai ya fito toilte ɗaure da towel a ƙugunsa kenan ta shigo kamar wacce aka jeho ta ba tare da ta yi sallama ba, ɗauke kanshi yai daga kallonta ita kuwa ganinsa a haka ya sa ta ji wani yanayi matsowa ta yi kusa da shi ba tare da ta ce komai ba bayan idanunta da ke yawo a jikinsa kaucewa yai domin ya lura so da abin da take son yi, sai dai duk yanda ya so ƙin abin sai da ta samo kanshi domin ta yi matuƙar kewarsa da ma shima a 'yan kwanakin nan haƙuri yake musamman ma idan ya je gurin Nuriyya duk sai ya ji shi a takure nan fa suka lula duniyar sama sai da ta fara mishi ƙananun mita kafin ya ƙyaleta tare suka shiga wanka sai da ya sake kimtsawa sannan ya zauna yana kallon yanda take ta murmushin yaƙe ga dukkan alamu kuma akwai abin da take son faɗa masa sai dai yanda ya yake ɗauke kai tare da sake tamke fuskarsa ne ya hanata yin magana. Abinci ta zuba mishi tana kallon yadda yake komai a nutse wannan yanayin nasa ba ƙaramin burgeta yake yi ba. Wani murmushi ne ya suɓuce mata wadda ita kanta bata san na mene ne ba, ɗagowa yai yana kallon yadda take murmushi har sautin sa yana fita wanda rabon da ya ga irin haka a ɗau shekaru masu yawa "To fa! Wannan murmushin fa?" Ya tambaye ta tare da ajiye cokalin gyara zama ta yi tare da faɗin "Ina kallon kyakkyawan fuskar mijina mana, gani na yi ka ƙara kyau da cikar haiba, nutsuwarka ya sake ƙaruwa fiyye da na baya gaskiya ba ƙaramin dace na yi ba.."
"Dacen me?" Ya katse ta da faɗin haka "Samun gwarzon kamar ka mana" Wani murmushi yai tare da ture abincin gefe yana fuskantar ta ganin haka ya sa ta nutsu sosai tare da ƙura masa ido.

"Tun kwanaki na so in faɗa miki abin da ke faruwa sai dai kika ƙi ba ni damar hakan duk yanda na so mu yi maganar sai ki kauce da kawo min uzirin kina busy" Ɗan dakatawa ya yi tare da fesar da numfashi dan ya san halin abar tasa akwai ta da birkicewa musanman ma a kan batun kishiya. "Hmmm! Ina sauraron ka" Ta faɗa tana jin hawaye na cika mata idanu ya tabbata dai maganar aurensa da gaske ne kenan?
"Wata takwas kenan da Umma ta yi mini.." Ganin yadda ta zaro idanu tana kallon shi ne ya sa shi yin shuru "Ka yi shuru ka ci gaba da maganar ka" Murya a karye ta ƙarasa maganar tare da runtsa ido "Ta yi min aure" Buɗe idanuwanta ta yi da sauri nan hawaye suka zubo mata "Aure fa ka ce? Kai ƙaramin yaro ne da Umma za ta yi maka aure ba tare da akincewarka ba? Shi ya sa kake ta inda inda kana kauce min , kwana biyu ba ka kirana bare ka ji ya nake ashe aure ka yi kana can kana shagali da amariyarka wallahi sai Allah ya saka min zalunta ta da ka yi munafuki wai an maka aure ai ko yaro ba zai ɗauki wannan maganar taka ba bare ni da girmana da hankali na ka dinga faɗa min zancen da hankali ba zai ɗauka ba.."
"Ya isa haka! Ban son wani dogon magana dan Allah aure na ce miki an yi min ni ma ban sani ba sai da ta gama komai take sanar mun.." Cike da ɓacin rai ta dakatar da shi tana faɗin "Ka ce dai sai da kuka gama komai naku kake sanar min, munafuki ai dama haka halinku yake ba za ku taɓa iya canzawa ba, ba de aure ka yi ba? Hmm! Wallahi ka kuskura ka kawo wata 'yar isa gidan nan se na ƙona ku daga kai har ita in ba munafurci ba me ya sa ba a bari an yi auren a gaban idona ba sai da ba na nan shi ne za a rufe ni saboda ba a sona? Allah ya fiku kuma zai

saka min wallahi ba zan ya fe ba!" Duk sai ya ji babu daɗi ganin yadda take ta ihu tana faɗin Allah zai saka mata kenan zalunci ne dan ya yi aure? Me ya yi mata da zafi take haɗa shi da Allah, shi ba mutum ba ne me son hayaniya da maimaita magana duk abin da aka danganta shi da Allah yana jin lallai lamarin ya girmama. Cike da sanyin jiki ya biyo ta ɗakinta yana rarrashinta tare da bata haƙuri haka yai kiɗinsa yai rawarsa ba tare da ta kulashi ba. Ƙarshe ma fita ta yi a gidan ta nufi gidan Honourable Sa'id da niyar sauke masa kwandon bala'i harda matar tasa domin duk da haɗin bakinsu aka munafurce ta. Suna sane da yadda ta tsani maganar kishiya amma babu wanda ya sanar mata kowa ya yi gum da bakinsa aikuwa sai ta tashin kan kowa har ita me ɗaure mishi ƙugu (Hajiya Umma).

Nuriyya zaune kusa da Amrah yayin da Zaliha take nunawa Momy Salamatu turarukan da suka kawo mata wadda Honourable Sa'id ya saya. Kallon Amrah Momy ta yi tana faɗin "Ku shiga daga ciki mana tun da taƙi sakewa a nan ɗin, ina ga can zata sake" Ta faɗa tare da kallon yadda Nuriyya take ta sunkuyar da kai tamkar wacce take gaban surukanta. Hannunta Amrah ta kama suka nufi ɗakinta "Dalla malama ki saki jikinki duk kin bi kin takura kanki haka za ki je kina yi wa Dad ɗin mu?" Murmushi kawai ta yi tare da kwanciya saman katifar "Wai Noor wani irin wulaƙanci ne haka, mutum yai ta miki magana ba za ki ce komai ba  sai murmushi.." Zaune na miƙe ina mamakin abin da ta ce "Uhm ai kin fi kowa sanin yadda nake" Ɓata rai Amrah ta yi tare da faɗin "Bari in kira Dady ya zo wataƙila za ki yi magana.." Ai da sauri ta ce "Dan Allah ƙyale ni da wannan maganar ni bana so ya dinga zuwa inda nake"
"Akan wani dalili? Mijinki ne fa" Amrah ta faɗa tare da zaro ido "Ni dai dan Allah ki bari kada ki kira shi" Miƙewa Amrah ta yi tare da jan glass ɗin window tana kallon motar da ya shigo "Taɓɗijam! Lallai akwai daru Momy Larai ta dawo kenan" Ta faɗa cikin ranta tare da rufe Window kiran Alh. Aminu ta yi domin shi ya ce ta ɗauko mishi Nuriyya.

"To munafukai shi ne aka munafurce ni Salamatu ashe har da ke za a haɗa baki a yi mini kishiya? Wallahi tun da Aminu ya yi aure Sa'idu ma zai yi aure Allah ya isa tsakani na da ke.." Da sauri Momy Salamatu ta ce "Zaliha shiga ɗakin su Khadijah ina zuwa" Tana barin wurin ta ce "Haba Larai me ye haka? Ya za ki shigo ba sallama sannan kina kirana da munafuka yaushe na san an yi haka? Hajiya Umma ita ta yi wa mijinki aure dan Allah karki tada hayaniya da yara a gidan..."
"Eh ai dole za ki ce haka tun da an haɗa baki da ke wallahi ki faɗawa Sa'idu za mu gamu Allah sai na ci masa mutunci munafuki dan na san duk da sa hannunsa" Rufe baki momyn Amrah ta yi tana ƙoƙarin danne dariyar da ke son ƙwace mata "Dan Allah Aminiyar zauna mu yi magana duk ba abin tashin hankali ba ne.." Dakatar da ita ta yi da faɗin.
"Babu wani zaman da zan yi a gidan munafukai" Cike da zolaya Maman Amrah ta ce "Haba uwargidan Aminu.." Fuuu Hajiya Larai ta yi wucewarta tare da jan tsaki me Maman Amrah za ta yi ban da dariya ai gwara ma da Nuriyya bata falon domin wallahi zata raina mata dan wannan hauka ne take yi ba kishi ba, Allah ya sa ma ɗakin Amrah akwai tazara ba za su ji wannan ɓaɓatun nata ba. "Allah ya kyau" Abin da ta ce kenan sannan ta kira Zaliha suka ci gaba da lissafin turaren kasancewar ita ma yanzu ta shiga business ɗin turarukan tana bawa Maman Nafisa kuɗi a kan ta dinga yi mata masu kyau aikuwa jama'a na saya sosai dan harda haɗi na musamman take siyarwa.

Kallon Amrah da ke ƙoƙarin fita ta yi tana faɗin "Ina za ki je?" "Yanzu zan dawo" Abin da ta ce mata kenan sannan ta fita a ɗakin. Tana dariya saƙo ta turawa Dady sannan ta koma falo ta samu Mamanta har yanzu suna lissafin turaren.

Kwanciyar rub da ciki ta yi tana duba hotunan su na makaranta wadda ta gani a ɗakin bata ji motsin shigowarsa ba duk da yai sallama ciki-ciki hakan bai sa ta farga ba, kasancewar hankalinta yai nisa tsaye yai yana bin bayanta da ido ganin yadda ta ko'ina ta cika mace kasancewar ta cire hijjabinta lokacin da ta idar da Sallar la'asar tana da diri me kyau da ɗaukan hankali babu abin da ya fi mayar da hankali kamar bayanta mazaunanta sun fisgeshi sosai wani irin lumshe ido yai domin doguwar rigan yadin material ne a jikinta dalilin da ya sa ya kwanta a jikinta har ya fitar da mazaunanta kenan. Motsin da ta ji ne ya sa ta faɗin "Lallai Amrah kin iya ajiyar hoto yanzu harda wanda muka ɗauka a waya kika wanko su..." Ɗif ta ɗauke maganar tata sakamon jin saukan numfashin sa gab da ita yana faɗin "Muga hoton.." A zabure ta watsar da su tana ƙoƙarin neman abin da zata kare jikinta da shi. Sai dai hijjabin na ƙasa nesa da su, ƙoƙarin sauka a gadon ta fara yi domin ɗauko hijjabin yadda take motsi da ƙoƙarin sauka ne ya sa shi ƙura mata ido ganin yadda jikinta ke rawa komai Tabarakallah Ma Sha Allah. Hannunta ya riƙe tare da mayar da ita ya zaunar da ita a jikinshi da sauri ta fara ƙoƙarin janye wa daga jikinshi lumshe ido yai jin yanda hannunta ke da mugun laushi tamkar auduga, tsam ya rumgumeta a ƙirjinshi yana shaƙar ƙamshin jikinta wanda yake sake birkita mishi lissafi. "Dan Allah ka yi haƙuri ban san ka shigo ba ne.." Ɗif maganar tata ya ɗauke jin saukan numfashinsa bisa wuyanta wani irin dirirr jikinta yai kamar wacce aka tsikara da allura sai zamewa da rawar jiki take a ƙoƙarinta na son ƙwacewa daga riƙon da yai mata sai dai bata san sake rikita shi take ba kasancewar yadda jikinta ke gugan nashi ga tafin hannayenta da ke taɓa cinyarshi wanda ya sa shi sake susucewa yana sauke mata wani irin zazzafan kiss me rikitarwa gabaɗaya sai kai shi ya kwance jin yanda ko'ina na jikinta ke ɗauke da ƙamshi me fisgar hankali.
Wani irin numfashi yake saukewa tare da ni man bakinta wanda yake tsuke yayin da idanuwanta ke rufe tana fitar da wani irin numfashi na firgicewa da ƙyar ya iya kai bakin shi saitin kunnenta tare da yin magana cikin wani irin yanayi da sanyi ya ce "Yi haƙuri to" Buɗe idanuwanta ta yi tare da ture shi gefe tana mayar da numfashi bayan ta rarumo hijjabin ta saka nan ta sake duƙunƙune jikinta tare da fashewa da wani gigitaccen kuka tana jin kanta na juyawa. Da sauri ya matso yana shirin taɓa ta cikin tashin hankali ganin yadda take rawar jiki "Ki yi haƙuri ni kaina ban san na aikata miki hakan ba.."
Zubur ta miƙe tana neman hanyar fita, ganin yadda take a birkice ne ya sa shi saurin kamo ta domin muddin ta fita cikin wannan yanayin za a iya samun matsala. "Ki nutsu mana bai da ce ki fita cikin wannan yanayin ba.."
"Dan Allah ka daina bana so! Ka daina kusanto inda nake ba zan iya maka komai ba, ba ni da wannan ƙarfin da zan maka abin da kake.."
"Ban nema wani abu ba, kuma ba zan ƙara miki irin hakan ba I'm sorry..." Ya yi maganar cikin sanyi bayan ya zaunar da ita, Miƙewa yai yana kallon yadda har yanzu taƙi ta kalleshi wayarta ya ɗauka ba tare da ta sani ba sannan ya fita a ɗakin. Tana zaune shuru har Amrah ta shigo tana mata magana ba tare da ta sani ba dafata ta yi tana faɗin "Noor wai lafiyar ki lau kuwa? Tun ɗazu nake magana kin yi shuru me ke faruwa?" Wani irin numfashi ta sauke tare da miƙewa tana faɗin "Zan tafi gida yamma ya yi.." Ba tare da ta ji ƙarshen zancen nata ba tari

numfashinta gurin faɗin "Ok Daddy na jiranki gurin mota and ni ma zan zo after saboda maganar tafiyar da za ku yi.."
"Wacce tafiya kuma?" Cike da mamaki Nuriyya ta dakatar da ita kallonta Amrah ta yi sannan ta ce "Au na manta fa, Maman bata sanar da ke Daddy ya ce jibi za ku wuce tare ba?.."
"Dan Allah ki yi mini magana yadda zan fahimta ya ce za mu je ina?.."
"Zai je Ghana shi ne ya ce ki shirya daga nan sai ku je asibiti domin a duba lafiyar.."
Jagwab! Ta koma ta zauna tare da zare ido tana faɗin "Please dan Allah babu fa inda za ni tare da shi, koma waye ya shirya wannan tafiyar bafa zanje ba" Daga haka ta fito a ɗakin sannan ta je ta yi wa Maman Amrah Sallama koda ta je wurin motar gidan baya ta nufa sai dai tun kafin ta buɗe ta ji sautin muryansa inda yake faɗin ta shigo gidan gaba.
Ba dan ranta ya so ba ta shiga haka ya kawo su gida Zaliha na fita ya ƙulle motar tana ta kiciniyar buɗewa amma shuru ɗan juyowa ta yi ta kalleshi ganin yana danna wayarsa ne ya sa ta faɗin "Uhm motar a ƙulle fa yake.."
Ɗagowa yai yana kallonta tare da faɗin "Uhm ina sane da hakan" Yana gama faɗar hakan ya ci gaba da amsa waya inda suke tattaunawa kan tafiyar da zai yi, yanayin yadda yake maganar ta lura tafiyar me muhimmanci ne domin ya nutsu yana zuwa jawabi cikin nutsuwa da kyakkyawan turanci kamar baturen Faransa. Ya ɗauki a ƙalla minti talatin kafin ya sauke wayar zuwa lokacin kam ta gaji da zama ta yi kicin-kicin da fuska ga shi taƙi yi masa magana shi kuwa so yake lallai ta yi masa magana ganin bata da niyar maganar ne ya sa shi kwantar da kujeran motar yana lumshe ido ganin haka ya sa ta juyowa kamar zata fashe da kuka ta ce "Hmm zan tafi ana sallah fa" Wani irin murmushin gefen baki yai tare da faɗin "Ki shirya jibi za mu wuce.." Bata tsaya saurararon zancen nasa ba ta yi shigewarta cikin gida, a anguwar yai Sallar magariba tare da Baban su inda yake sake jaddada masa maganar tafiyar tasu sun taɓa hira kafin ya ba shi kuɗi, ya so ya sake ganinta sai dai lura da tana cikin fushi ne ya sa shi shiga mota leƙowa Baban su yai ganin bai tafi ba yana faɗin "Ba ku yi sallama ita ba ne a turo ta?" Ɗan murmushi kawai yai tare da girgiza masa kai sannan ya bar Area ɗin.
Zama ta yi jikin Maman su tana  sauke ajiyan zuciya, zame jiki Maman Nafisa ta yi tana faɗin "Mene ne haka? Sai ka ce wata jinjira kin zo kin wani danne min jiki" Ɓata fuska ta yi tana faɗin "Mamanmu idan ban zauna jikinki ba a ina zan zauna? Ai gwara na ji ɗumin uwata"
"Mijinki ya ce ki shirya za ku tafi jibi"
Sunkuyar da kanta ta yi tana jin hawaye na shirin zubo mata "Mamanmu ni ɗaya haka zan bi shi?" Ta yi maganar tana kallonta miƙewa Maman su ta yi domin bata cika son dogon magana dangane da maganar mijin ɗiyar tata ba, domin kunya take ji. Wani irin murmushi Fiddoh da ke kwance ta yi domin kunya irin na Maman tasu ba ƙaramin dariya yake bata ba.
"To sai a shiryawa ɗiya abin da ya da ce, domin da miji zata tafi, gwara tun yanzu a fara koya mata dabarun riƙe mijin tun da an ce kishiya gareta kuma..." Dakuwa Maman su ta yi  mata tana faɗin "Ungo nan na ce haba! Wai Firdausi wannan bakin naki ba ya shuru ne kam?" Ya mutsa fuska ta yi tare da nufar gurin kayanta dan zaman gidan ya gundureta haka, duk da zuwa take yi bata cika kwanan gidan ba, zuwan Amrah ne ya dakatar da ita inda suka shiga tattaunawa domin Daddy ya bata kuɗi akan ta yi wa Nuriyya siyayya nan fa suka fita tare dan Nuriyya tana can tana ihun babu inda za ta bishi. Kasuwa suka shiga inda suka shiga mata siyayyan wasu 'yan iskan kayan da da su da babu duk ɗaya, su kansu suna dariya ganin irin kayan da suke zaƙulo mata duk babu na arziki gefen underwear ma ba'a magana, haka suka jido mata kaya

sosai sannan suka dawo gida ko kallon su Nuriyya ba ta yi ba, domin duk haushin su take ji.

****

Tana zaune a falo yai Sallama ya shigo "Barka da dawowa" Fuska a sake ya amsa mata tare da faɗin "Barkanmu dai" sannan ya nufi ɗakinsa bin bayanshi ta yi tana ƙoƙarin taya shi cire kayan shi dakatawa ta yi jin baƙon turare a jikinsa ƙoƙarin daurewa ta yi sannan ta je ta haɗa mishi ruwan wanka yana shiga ɗaki ta fara binciken wayarsa ko zata samu Number yarinyar sai dai ko'ina na wayar tasa a ƙulle yake, tsaki ta yi tare da fita a ɗakin tana cin alwashin tarwatsa duk wani abin da ya danganci wannan kishiyar da aka yi mata koda za ta yi yawo tsirara sai ta hanata shigowa rayuwar mijinta uban 'ya'yanta , domin Aminu nata ne ita ɗaya babu macen da ta isa ta taɓa shi muddin kuwa ta yi gigin hakan sunanta 'GAWA' domin tana matuƙar son mijinta tana kuma kishin sa.
Abinci ta haɗo ta kawo mishi ɗaki abin da aka jima ba'a yi masa ba, aikuwa ya ji daɗin hakan sosai ganin yadda lokaci ɗaya ta watsar da mahaukacin kishin nan nata tana tarairayarsa tare da janshi da hira, duk wannan abin da take tana so lallai ta ji labarin Amariyar tasa ne sai dai ko kusa bai ɗauko zancen Nuriyya ba, duk yadda ta kai ga son jin wacece ita bai bata wannan damar ba, ƙarshe ma shuru ta yi tana tunanin yadda za ta yi ta gano inda yarinyar take nan yake sanar mata maganar tafiyar da zai yi, fatan alkairi da samun nasara ta yi masa sannan ta fita a ɗakin koma nata da niyar yana tafiya za ta je ta ɗauko Suhaima ta dawo gida. Yana gama kimtsawa ya kwanta zuciyarshi fal tunaninta shi kaɗai yake murmushi tare da shafa ɗan sajensa wanda suke kwance luf-luf, ga shi ya ɗauke mata waya bare ya kira ya ji muryanta duk da idan ya kira ma ba magana take mishi ba, se dai ta manna wayar a kunne tana jinsa har bacci ya ɗauke ta kafin yake ƙyaleta.

Wannan Littafin na kuɗi ne domin kasancewa cikin group ɗin za a tura ₦500 ta wannan account 2389596965 Aisha jubreel Zenithbank. Sai a tura shedar biya ga wannan Number 09079740079

#Amnoor
#Sadstory
#Destiny
#Hotlove
#Romance
#Sexstory
[5/9, 11:44 PM] FARHATULKALB💔🤗: *♡AMNOOR...!*
_A romantic story_
Wattpad: ayshajb
Arewabooks:ayshajb
®
FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION📚
★F. W. A★

Free page 25_26

Kuje YouTube ku yi Subscriber Channel ɗi na FARIN JINI HAUSA TV. Domin samun ƙayatattun littafanmu.

H-P Place Group.

Washegari yana idar da Sallar Asubahi ya nufi gidan Umma nan yake sanar mata tafiyar gaggawan da zai yi zuwa Ghana amma zai ɗauki Nuriyya su tafi tare domin yana son danganta ta da likita cikin jin daɗin kalamansa ganin ya sauko har ya karɓi aure kuma ga shi za su tafi tare da ita nan ta shiga sanya mishi albarka cike da jin daɗi shima ya dawo gida bayan ya kammala karin kumallo Laraba ta rako shi wurin mota inda drive ke jiranshi tana mishi addu'ar dacewa tare da buɗi mai amfani.
“Allah ya tsare min kai mijina uban ’ya’yana Ubangiji ya ba ka halal ɗinka Allah ya tsare ka da duk wani abun ƙi, Allah ya haɗa ka da alkairi zan yi kewar ka sosai” A bazata kalaman nata ya ratsa kunnuwansa da murmushi ya amsa tare da riƙe hannunta yana murzawa cikin nashi kana ya yi mata kiss sannan ya shiga motar yana ɗaga mata hannu ita ma bye bye ɗin take masa fuska cike da annuri. Motarshi ya ɓacewa taja wani dogon tsaki tare da shigewa cikin gidan Lagos zata koma wurin ƙawarta Fumi domin neman mafita dan ba za ta ƙyale shi da wannan matar da ya auro ba.
Tun jiya da dare Mamanmu ta hanani saƙat da wasu turarukan tsungunno tare da ciye-ciyen wasu abubuwan da ban san na mene ne ba, in zan yi magana sai ta dakatar da ni taƙi ba ni damar da zan tambayeta kayana kuwa tun daren jiya Fiddoh da Amrah wacce anan ta kwana suka gama kimtsa min suna dariya ba tare da na san tsiyar da suka tsuka mini ba, kasancewar na yi tsifa ya sa Zaliha ta tasa ni a gaba sai da ta yi min ƙananun kitso domin ita gwana ce wurin kitso Firdausi ce ta iya lalle Amma duk ta watsar kasancewar bata ba abin muhimmanci ba, ni kaina yadda ta zizara min kitson ya yi matuƙar burgeni, sai kusan ɗaya da rabi na dare muka kwanta da Asuba na fara neman wayata nan Amrah take sanar mun wai yana wurin Daddy shuru kawai na yi har gari ya waye ina ji suna magana da shi a waya inda yake sanar mata ga shi nan zuwa su fito. Kallo na ta yi ganin yadda na yi kicin-kicin da fuska domin wallahi ba ƙaunar tafiyar nan nake ba, dariya kawai Firdausi ta yi tare da gyara kwnaciyarta tana faɗin.
“Mamanmu idan sun tafi Allah ya tsare wallahi na gaji ba zan iya wani rakiya ba, Aunty Nuriyya Allah ya kiyaye ya tsare hanya Please ki kula ki dinga sake mishi fuska kina yi mishi magana ki aje kurmancin nan a gefe ki lallaɓa mijinki domin kishiya gareki ki yi ƙoƙarin kame zuciyarsa a ɗan tafiyar nan da za ku yi..” Sai ta yi shuru tare da lumshe ido kana ta ci gaba da magana "A baya naji haushin Babanmu amma ganin yadda wannan mijin yake miki abin arziki harda ƙoƙarin samar miki da lafiya ya sa naji sanyi, domin ga dukkan alamu zai kula min da ’yar’uwata zai ba ki farinciki ni ma Allah ya sake haɗani da Alhaji na..” Ta ƙarasa maganar tare da yatsina fuska. Hararanta Nuriyya ta yi domin duk kalamanta haushi ya bata. “Yanzu Mamanmu ba za muje tare ba? Ni ɗaya kawai?” Ta yi furucin hawaye na gangaro mata ɗauke kai Maman Nafisa ta yi tare da faɗin. “Ki tashi ku tafi naji dirin mota Allah ya tsare ki kula da ibadarki!” Daga haka ta fita a ɗakin domin yanayin da Nuriyyan take yi za ta iya sakata kuka ita ma.
“Noor yau Alhamis kina azumin ne?” Amrah ta yi mata wannan tambayar tana miƙawa Zaliha jakar kayan ta kai wurin motar. Gyaɗa mata kai ta yi alamar Eh, leƙowa ta yi tana kallon Daddy

da ke zaune gidan baya. “Daddy barka da safiya” Idanunshi na kan Nuriyya ta amsa mata sannan ya buɗe mata motar, juyowa ta yi tana kallon Amrah hawaye na ƙoƙarin zubo mata “Amratu kema ba za ki kije ba?” Murmushi ta yi tare da faɗin “Zan zo mana amma sai kun fara tafiya zan biyo ku, Dan Allah Noor ki kula min da Daddyna kin ji?”
“To sai kin zo” Share mata hawaye Amrah ta yi sannan ta miƙa mata jakarta na rataye kana ta shiga motar sai da motar ya ɓace sannan Amrah ta koma cikin gidan tana jinjina halin irin na Noor tun da wannan lamarin ya faru da ita shuru-shurun ta ya ƙaru fiyye da na baya.
Juyowa yai yana kallon yadda ta juyar da kanta gefe tana kallon waje, hannunshi ya ɗora saman cinyarta a hankali ya furta “Barka da safiya” Duk sai taji kunya ya kamata bai kamata babba da shi ya fara gaisar da ita ba, bayan kuma ita ce ke ƙarƙashin ikonsa murya a sanyaye ta ce “Barkanmu da safiya” Daga haka bata sake cewa komai ba. lokaci-lokaci yakan waigo ya kalleta har barci ya ɗauketa, ya yi mata siye-siyen kayan ciye-ciye sosai sai dai bata ci ko ɗaya ba, da ya takura ta ta sanar masa da azumi take. A hanya ta sha ruwa shima ba wani abun kirki ta ci ba sai da ya takura ta sannan ta ci abincin kaɗan.
Tun kafun su isa ta fara jin wani irin sanyin da ya fi na Abuja kasancewar ana tsaka da hunturu dole sai da ya nema mata suwaita ganin yadda take rawar sanyi duk da tana cikin hijjabi tun a Lagos suka rabu da driven shi. Hotel ɗin da ya kama ɗaki ɗaya ne koda suka shiga da ƙyar ta yi sallolin da ke kanta sannan ta yi wanka da ruwan zafi, kasancewar ya fita a daƙin ya sa ta yi komai cikin gaggawa domin bata so ya shigo ya sameta bata gama shiryawa ba, wani abincin yai musu order bata wani ci sosai ba ta kwanta kan doguwar kujeran da ke ɗakin tare da rufe jikinta da bargo kayan jikinta ma bata sauya ba, sai dare sosai ya shigo sannan ya yi wanka yana cin abinci yana kallon yadda ta tsakura kanta a kujera 2str murmushi kawai ya yi sannan ya ɗauketa ya ɗorata saman gado yana kallon kyakkyawan siririn fuskanta kana  shima ya kwanta tare da rufe musu jiki gabaɗaya. Karfe huɗu da rabi ta farka tana salati da sauri ta matsa gefe ganin suna gab da junansu. Jin motsinta ya sa shi buɗe Idanunshi da ke cike da barci “Ya dai?” Ya ce yana ƙoƙarin kamo hannunta sauka ta yi tare da nufar toilte ta ɗauro alwala tana fitowa shi ma ya shiga bayan sun idar da Sallah kanta a ƙasa ta ce mishi “Ina kwana?”
“Kwana yana inda yake, kin tashi lafiya? Ya gajiyan hanya?” Matse hannunta ta yi tare da faɗin “Alhamlillah” Ƙaramin ƙur'anin da ke jakarta ta ɗauko tare da hayewa saman kujeran tana karanta sautin muryanta na fita kaɗan-kaɗan. Lumshe Idanunshi yai yana ci gaba da sauraron sautin daddaɗan muryanta, ƙarfe shida ta rufe karatun a fakaice ta kalleshi ganin yana ƙoƙarin cire kayanshi ne ya sa ta ɗauke kanta daga kallonsa toilte ya shiga yai wanka ya fito ɗaure da babban towel a ƙugunsa tana tsaye jikin tagar window tana kallon yadda garin yai hazo ga raɓa na sauka. Wurinta ya ƙaraso tare da kwantar da kanshi a kafaɗarta ƙamshin sabulun da yai wanka da shi ne ya daki hancinta a hankali ya shigar da hannayenshi cikin hijjabinta tare da laluɓo hannunta yana murzawa cikin nashi murya can ciki ya ce “Me kike kallo?” Shuru ta yi tare da janye jikinta daga na shi. Alamar mutum ya gani a bakin ƙofar nan ya ƙarasa ya karɓo musu breakfast ɗin da yai musu order saman daining ɗin ya ajiye abincin yana juyawa ya ga ta nufi toilte wanka ta yi tare da wanke kayan da ta cire, hijjabinta ne kawai ta bari tana gamawa ta ɗaura babban towel bayan ta yi brush ta tsaya bakin ƙofar tana jin kunyar fitowa saboda rashin sabo waigowa yai jin motsi kuma bata ƙaraso ba, yana ɗaura agogo ya yafito ta da hannu a hankali ta fito ta nufi inda jakar kayanta yake tana buɗewa ta fara bin kayan da kallo ganin wasu

irin tarkacen kayan 'yan iskan da aka tara mata cikin jaka, wani baƙinciki ne ya tokare mata ƙahon zuciya, duk cikin kayan babu na arzikin da zata iya sakawa wasu irin tarkacen gajerun riguna da ƙananun skirt sai wando iyakar cinya, sai shimi marasa hannu, ji ta yi kamar tasa hannu a ka ta fasa ihu. Shi kuwa yana zaune yana jira ta zo su karya saboda fitar da zai yi, gyaran murya yai tare da faɗin "Ki shirya ki zo kar abincin ya huce"
"Ina wayata? Ina son magana da Mamarmu" Ta faɗa tare da miƙewa ta nufi bayi domin saka rigar da ta samu wanda bai gama rufe cinyarta ba, yana da siririn hannun ga shi ya manne a jikinta sosai turaren da Maman su ta saka mata ta shafa tare da mayar da hijjabin sannan ta fito ta zauna nesa da shi. Abincin ya zuba musu tare da faɗin "Oya zo muci" A ɗarare ta zo ta zauna kusa da shi suka fara cin abinci wadda kaɗan ta ci domin tana jin bakinta babu ɗanɗano, yana gama ci ya miƙe ya kalleta sannan ya ce "Ni zan fita akwai abinda kike buƙata ne?" Girgiza mishi kai ta yi alamar a'a wayarshi ya ɗauka tare da faɗin "Sai na dawo" Gyaɗa mishi kai ta yi ba tare da ta kalleshi ba, haka ya fita yana faɗin ta ƙulle ƙofar reception ɗin hotel ɗin ya nufa ya ba da sallahun abinda za'a kai mata da rana sannan ya nufi inda za su yi meeting. Tagumi ta yi tana tunanin yadda rayuwa yake shirin sauya mata daga ƙunci zuwa wani yanayi na daban, ganin tunanin ba zai fisheta da komai ba ne ya sa ta ɗauki alƙur'ani tana karantawa har barci ya ɗauketa. Bayan azahar ta farka nan taga an ajiye mata abinci tuwon semo da miyar agushi brush ta sake yi sannan ta nufi gurin abincin domin al'adanta ya zo babu damar yin Sallah. Tana gamawa ta sake kwanciya sai bayan magariba ya dawo tana kwance ta ji ana ƙwanƙwasa ƙofar "Waye?" Ta ce tare da miƙewa tana saka hijjabinta "Zo ki buɗe" Jin muryansa ya sa ta zuwa ta buɗe mishi ƙofar Hoggin ɗinta yai yana faɗin "Yi haƙuri na barki ke ɗaya" Zame jikinta tai tana faɗin "Sannu da zuwa" Can ƙasar maƙoshinta ta yi maganar. Wanka ya shiga a gurguje sanan ya yi sallah suka ci abinci washegari ma haka y afita bai dawo da wuri ba, ya jera kwana huɗu yana fita gabaɗaya ta gaji da zama shuru ga shi ya ƙi bata wayarta so ɗaya suka yi magana da Amrah ta wayarshi tana kwance shuru ya shigo a gajiya zama yai gefenta tare da sauke gwauron numfashi yana faɗin "Talaka bawan Allah" Ba ta juyo ba yau ko sannu da zuwan ma bai samu ba "Ya dai?" Ya ce yana leƙa fuskarta kuka ta fashe da shi tare da faɗin "Ni ka kaini gidanmu" Yadda take maganar ne ya so ba shi dariya, da ƙyar ya daure yana faɗin "Sorry ba ga ni ba? Yi haƙuri ba zan sake fita ba okay?"
"Ni dai a'a gida zan koma" Jin fitar sautin zazzaƙan muryanta ya sa shi lumshe ido kana ya buɗe yana kallonta toilte ya shiga yai wanka tare da alwala ya gabatar da Sallar isha wanda bai samu ya yi kan lokacinsa ba, sanyin ya ɗan ragu kwana biyu dalilin da ya sa ya rage kayan jikinshi ya saura daga shi sai gajeren wando da ƙaramin rigar shan iska, abinci ya ci sosai sannan ya dawo kan gadon zai kwanta matsawa ta yi gefe tare da gyara bargon ta sake rufe jikinta dan yau ta wanke hijabinta matsowa yai sosai kusa da ita tana ganin haka ta sake matsawa still ya sake matsowa ita ma bata gaji ba ta matsa a haka har ta kai ƙarshen gadon, ɗan murmushi yai tare da shigar da hannayenshi cikin bargon yana shafo cikinta wanda yake nan a shafe wani irin dirr jikinta yai tana son janyewa ta kasa saboda ya zagayeta da hannayenshi tare da shigar da kanshi wuyanta yana shaƙam ƙamshin turarenta tare da rufe ido yana fesar da numfashi shiga cikin jikinta yai sosai yana ƙoƙarin kai hannunshi rigarta da wani irin rawar jiki tasa mishi ihu tana shirin zamewa bakinshi ya kai nata a hankali yake fitar da numfashi wani irin yanayi ya shiga lokacin da ya manna bakinshi kan nata take ya fara jin notikan kanshi na kwancewa yana shirin barin duniyar da yake zuwa wata duniyar. Wani irin

ajiyan zuciya yake saukewa jin yadda take motsawa tudun ƙirjinta na taɓa shi. A razane ta fasa wani irin ƙara nan take jikinta ya fara kakkarwa kamar zata shiɗe, da ƙyar ya iya dakatawa yana jin kanshi na wani irin sarawa saboda gajiyar da yake tattare da shi. Kallon yadda take rawar jiki idanunta na ƙakƙafewa yai, a hankali ya mirgina gefe tare da dafe kanshi tana mayar da numfashi washegari da wuri ya nufi asibiti da ita domin ba su iya barci ba saboda yanayin razana da take ciki koda suka dawo yana ta mamaki tare da juya kalaman likitan inda yake sanar da shi zata dawo daidai akwai abin da idan aka yi mata yake sa ta razana da shiga ɗimuwa ne wadda tabbas an taɓa tilasta ta ko an yi mata ba tare da amincewarta ba, wannan dalilin ya sa take shiga cikin wannan yanayin amma in har aka yi amfani da magungunan sannan aka bi ƙa'ida in sha Allah za ta dawo daidai. Idanu kawai ya zuba mata yana kallon yanda numfashinta ke sauka a hankali shafa fuskanta yai tare da yi mata kiss a goshi sannan ya kwanta yana ci gaba da tunanin abin da ya haddasa mata haka.

**

"Mijinki ya ɗauki kishiyar ki sun tafi yawon cin amarci kina ina har hakan ta kasance ina zafin kishin yake? Ni ba za a yi min kishiya ba ni ka za-ka za, kin san dai wannan mutumin ba zai yi min ƙariya ba, domin shi ne yake min aikin da nake juya mijina yadda nake so, shi ya yi mini aikin da na bazama kishiyata duniya wacce har yau babu ita babu labarin ta idan har kina son raba mijinki da ita ki samo sunanta, gashin kanta, da kuma farcen hannunta na hagu, sannan ki samo ƙasar da ta taka muddin kina so a yi miki mugum aiki a kanta abinda za ki yi kenan" Cewar ƙawarta Fumi "Daman tare da ita ya tafi? Ashe shi ya sa in muna cikin magana da dare ya ce zai kira suna tare? Taɓɗijam! To wallahi ko ma mene ne zan yi muddin zai dawo mallakina ni ɗaya!"

"Aunty Nuriyya amariyar Alhaji yaushe ne za ku dawo?" Cewar Zaliha da ke magana cikin wayar Maman su. Satan kallon shi ta yi tana jiran taji me zai ce mata dangane da komawarsu ganin sun shafe sati amma ba ya ma maganar komawa ɗauke kanshi yai tare da ɗaukar ɗayar wayarshi da ke ringing tun ɗazu ganin Laraba ce me kiran ya sa shi fita a ɗakin ajiyar zuciya ta sauke domin dai kiran matar shi ce yake sa shi fita a ɗakin "Zaliha ni ma ban sani ba, kullum in na tambaye shi ba ya min magana ya Mamanmu da Fiddoh? Ita dai Fiddoh bata riƙe waya bare mu yi magana ga shi ba zaman gida take ba, idan ta dawo ki ce ta kira sai mu yi magana" Zaliha ta ce "Mamanmu tana nan lafiya Fiddoh ta ce wai ta yi miki laifi ba za ta yi magana da ke ba har sai kun dawo za ta ba ki haƙuri ga Mamanmu ku gaisa" Manna wayar ta yi a kunnen Mamansu kasancewar hannunta na cikin turare ba halin ta riƙe. "Mamanmu! Na yi kewarku sosai wallahi dan Allah ki yi mishi magana mana mu dawo na fa gama shan maganin.." "Sannu Allah ya ƙara lafiya sai anjima aiki nake..." Da sauri ta ce Allah sarki Mamanmu ko ɗan hira ba ki so mu yi da ke?" Kallon Zaliha Maman Nafisa ta yi sannan ta ce "Nuriyya sai anjima" Zaliha ta ce "Aunty Dan Allah ki kawo min tsaraban dogayen riguna da ƙananun kaya..." Buge mata baki Maman su ta yi tare da karɓe wayar ta kashe. Ajiye wayar Nuriyya ta yi tare da sauke ajiyan zuciya duk hirar da suke yana jin su domin ya jima da dawowa ɗakin, "Kwanan nan za mu koma shi kenan?" Da sauri ta ɗago kai tana kallonshi tare da faɗin "Da gaske?" Ledar da ke hannunsa ya miƙa mata yana faɗin "Ki shirya za mu fita" Yana gama faɗar haka ya fita a ɗakin wanka ta yi tare da saka duguwan rigar ta yafa mayafin sa duk sai ta ji kunya domin bata saba

irin shigar ba, dan mayafinsa babu girma ɗan hoda ta shafa tare da man baki shigowa yai ɗakin da waya a kunnensa yana magana tsareta yai da ido ganin yadda ta yi bala'i kyau, rigar ya amshi jikinta ba abinda ya fi fisgarshi irin laɓɓan bakinta da ke walƙiya, "Ina zuwa zan kira ki" Ka she wayar ya yi da sauri tare da ƙarasowa inda take yana kallon fuskar tata, a bazata ta ji ya kai bakinshi kan nata yana tsotsa cikin wani irin yanayi yana fitar da numfashi riƙe rigarsa ta yi da ƙarfi tare da runtsa ido tana jin yadda yake ƙoƙarin shafo ƙirjinta da ƙyar ta ƙwace da ga hannunsa tana mayar da numfashi shi dai ba shi da wani aiki sai na matse mutum ta faɗa cikin ranta tana turo baki. "Ki gama zageni anjima za ki faɗa min.."
Gyara zama Emanuel ya yi tare da kallon Fiddoh da ke shan shisha tana  fesar da hayaƙi tare da lumshe ido, gabaɗaya ya kasa gane kanta dan kwana biyu taƙi kulashi ga shi ba ya jin daɗin mu'amula da wata mace bayan ita karɓan shishan ya yi daga hannunta yana kallon wasu shegun kayan da ta saka wanda suka gama bayyanar da jikinta, kwana biyu da kama musu ɗaki a hotel amma ba ta tsinana mishi uwar komai ba. “Fiddoh! Me ke faruwa ne? Ba ki jin tausayi na? Ki duba fa a matse nake look at this..” Ya ƙarasa maganar tare da kai hannunta kan sandar dake tsaye ƙyam. “Ni fa duk wani sha'awa ya fi ce min a rai, shi kaɗai kawai nake muradi, ALHAJI NA nake son gani shi ne wadda zan iya yi wa komai saboda ina mugun son shi!” Rumgumeta ya yi sosai a jikinshi yana shafa ta. “Very soon za ki ganshi” Za ta yi wani magana ya haɗe bakinsu wani irin mugun kiss yake mata tare da watsar da kayan jikinsu, sosai ya gigita mata lissafi kafin ya fara having sex da ita yana ihu jin ta ƙara Sweet “Ahhhhh....! Fiddooooo....Uuhhhhh... Thank you Beb!”
Yana moving da ita a Bed yayin da yake sucking breas ɗinta sai da ya samu cikakken awa guda a kanta kafin ya janye wani barci ne ya kwashe shi tana ganin haka ta zare jikinta tare da yin wanka ta fito tana jiran su Na’ila dan tare suke kowa na inda guy ɗin shi yake, kamar gizo kamar gaske ta ga me kama da Baban Suhaima murza idanunta ta yi tana faɗin “Allah ya sa yau ban shawu da yawa ba” Da gudu ta ƙara so tare da riƙe hannun shi, fitowarshi kenan daga mitin domin baƙi suka yi ya kama musu hotel, wayarshi na manne a kunnensa yana kiran Amnoor amma taƙi ɗaukar kiran don fushi take yi da shi da wani irin mugun sauri ya juyo yana kallon hannunshi da aka riƙe “Wacece ke?” Ya yi maganar fuska a ɗaure ganin yadda take tamkar tsirara ɗauke kanshi ya yi daga kallonta tana koran sheɗan cikin zuciyarshi “Haba Alhaji na ni ce fa masoyiyarka...” Wani irin ƙazamin kallo yai mata tare da faɗin. “Ina da kamilar mace! Wacce take mutuwar sona ni ma nake mutuwar ƙaunarta, babu abin da zan yi da ballagaza ƙazama irin ki”
Cike da takaicin kalamansa ta ce “Yau ko da mata huɗu gareka sai ka saki ɗaya ka aure ni, domin kaine tauraro na, da kai nake da burin rayuwa kuma dole ka aure ni wallahi muddin ka ƙi, na dinga bibiyarka kenan kuma sai na hana ka saƙat ni Mahaukaciya ce a kan abin da nake so! Za ka aure ni!” Ture ta ya yi tare da jan dogon tsaki ya shige motarshi direct gidan su Nuriyya ya nufa lokacin magariba ta gabato kiran wayarta ya yi cikin sa'a ta ɗaga murya can ciki ya ce “Ki zo ki amshi saƙo zan wuce...” Bai jira ya ji me za ta ce mishi ba ya kashe wayar fitowa ta yi tana duba ko Maman Nafisa na waje sai ta ga ba ta nan ajiyar zuciya ta sauke tare da dafe ƙirjinta tana jin zuciyarta na bugawa cikin sanɗa ta fara ƙoƙarin fita daga cikin kichin Maman su take kallon yadda take tafiya kamar munafuka tsaki ta yi domin yau za ta kawo ƙarshen iskancin nan nasu dan sarai ta lura da fitar da take da lokacin da take dawowa. Tana shiga motar ya kulle tare da barin anguwar “Daddy ban san me kake nufi da ni ba, na faɗa maka na gaji da wannan gantalin da muke akan titi dan Allah na gaji!”

“Wai ke ba ki tausayi na ne kam? Na ce miki zan yi duk abin da kike so Please ki bari na samu nutsuwa wallahi a matse nake kin san ba dai iya haƙuri na yi kwana tara fa ban ganki ba, ban ji ɗumin jikin ki ba, Dan Allah Amnoor ki bar wanna maganar har na nutsu” Yai maganar tare da jawota jikinshi yana matse ta dan yanayin Fiddoh ya ɗaga mishi hankali. Sai da ya samu nutsuwa sosai ita ma munafuka harda kuka tana faɗin ta yi kewarshi goma da rabi ya dawo da ita Maman Nafisa na jin dirin mota ta fito daga baƙin ƙofar tana kallon su. Fitowa ya yi tare da buɗe mata mota duk ba su lura da ita ba, ɗan rumgumota ya yi yana mata kiss tare da faɗin “Allah zan yi ƙoƙari a satin nan za ki tare...” Gyaɗa mishi kai tari sannan ta fito klalon Maman Nafisa ta yi tare da hadiye wani mugun miyau. “Koma ki bi shi ku tafi!”
“Maman mu..”
“Rufe min baki munafuka ke har kin yi wayon da za ki dinga satar hanya kina bin miji? Karki kuskura ki shigo gidan nan...” Shuru ta yi ba tare da ta ƙarasa maganar ba tana kallon Alhaji Aminu da ya juyo zai yi mata magana “Alhaji Aminu kai ne mijinta?” Kallon shi Nuriyya ta yi tare da kallon Maman su tana mamakin daman ba ta san mijinta ba? Amma ta yaya ta kira sunan shi kai tsaye ? da alamun dai ta jima da sanin sa...

Paidbook ₦500
09079740079

_Washh Allah na gaji wallahi_🙁

#Amnoo!
#Romance
#Sexstory
#Sadstory
#Sisterslove
[5/9, 11:45 PM] FARHATULKALB💔🤗: *♡AMNOOR...!*
_A romantic story_
Wattpad: ayshajb
Arewabooks:ayshajb
®
FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION📚
★F. J. W. A★

Free page 31_32

Ku je YouTube ku yi Subscriber Channel ɗi na FARIN JINI HAUSA TV. Domin samun ƙayatattun littafanmu.

H-P Place Group.

“Dan Allah Mamanmu ki yi haƙuri..” A fusace ta ce “Ungo nan, shashasha mara lissafi ai ni kin gama ba ni mamaki tun da har kin san dabarar da za ki yi ki bi miji kuna yawon gantalewa a titi,

na faɗa miki muddin kika yarda na ga ƙafarki cikin gidan nan zan saɓa miki. Ki bishi ku ƙarata can"
"Daddy ka gani ko? Ka ga irin abin da nake tsoro yanzu ta fusata wallahi ba za ta taɓa yarda ba tun da ta ce haka, ba ta canza magana..." Na yi furucin hawaye na zubo min shi kuwa ya ma rasa me zai ce mata, wani iri yake jin abin ya san idan Laraba ta san matar da yake aure 'yar mai aikinta ce akwai matsala. Fitowar Zaliha da jakar kayana shi ya sake tabbatar da Mamanmu ba za ta sauko daga dokin fushi ba, ina kallon shi ya ɗauki kayan ya saka a mota "Aunty Amnoor ku ta fi kawai, tun da ta ce haka kema kin san halinta bare yanzu ban san abin da yake saurin fusata Maman Nafisa ba, abu kaɗan za ka yi mata ta hau faɗa, ki yi haƙuri kawai" Juyawa ta yi ta koma cikin gidan tana ji ya kama hannunta tare da buɗe motar ya saka ta. "Sai ka ce mara gata? Wallahi Daddy duk kai ka ja min wannan abun, babu 'yan rakiya daga ni sai kai za mu ta fi..." Hannunta ɗaya ya kama yana jin yadda sautin kukanta ke taɓa zuciyarshi. "I'm sorry Amnoor, duk laifi na ne amma please ki daina kukan nan yana taɓa zuciyata" Kwantar da kanta ta yi a kafaɗarshi tana sheshsheƙan kuka yana daidaita parking motar ya buɗe mata tare da kamo hannunta dricet yai hanyar ɗakin shi da ita, zaunar da ita ya yi kan bed tare da riƙe hannunta cikin na shi "Ki yi haƙuri.." Gyaɗa mishi kai na yi ina danne kukan da ke shirin ƙwace min.  Fita ya yi daga ɗakin can sai ga shi ya dawo da kular abinci freezer ɗakin ya buɗe tare da kwaso tarkacen driks, duk wannan abubuwan da ya jere su gabana ban kalli ko ɗaya da niyyar ci ko sha ba, illa wani haushin sa da ya cika zuciyata. Kayan jikinshi ya cire tare da ɗaura towel a ƙugunsa, juyowa ya yi yana Kallonta kana ya ce.
"Tun da ba za ki ci abincin ba zo mu yi wanka" Kallon shi na yi tare da ɗauke kai dan na lura bai ma damu da damuwata ba, sai ma wani kallon da yake binta da shi. "Please..." Ya faɗa tare da kamo hannunta yana cire himar ɗin da ke jikinta, tare suka nufi toilte ɗin tana kallon ikon Allah ganin yadda aka tsara komai tare da narkar da dukiya. Saukan numfashinsa ta ji a wuyanta yayin da hannayen shi ya kasa zama wurin ɗaya, ta lura Daddy yana daga cikin fitinannun mazan nan ne wadda ko da za su kwana yin abu ɗaya ba zai gajiya ba, kunna musu shower ya yi tare da jan zip ɗin rigarta nan take yai ƙasa tsakiyar bayanta ya ci gaba da shafowa tare da ɓalle pin ɗin brezian ta. Shafo gashinta yai tare da haɗe fuskokinsu yana goga hancinsa saman nata. Ajiyar zuciya ta sauke tare da buɗe tsumammun idanunta tana kallon yadda yake lumshe na shi tare da sauke ajiyan zuciya. Tallafoshi ta yi tare da manna bakinta saman na shi, nan suka shagala da abu ɗaya sun jima sosai a toilte ɗin domin sai da ya juya ta ya ji ya samu nutsuwar da yake buƙata sannan suka yi wanka, ai tana fitowa ta sauka kan abincin da ya ajiye wanda har ya huce, sosai ta ci abincin domin cikinta tamkar wacce aka yashe. Kallonta yai tare da sakin murmushi sannan ya fita ɗakin Laraba ya nufo "Yaushe ka dawo? Na ga har ka yi wanka ka sauya kaya" Yana riƙe da hannunta suka zauna gefen gado. "Ban jima da dawowa ba, sai dai na ɗauko Amnoor.."
"Wacece kuma Amnoor?" Ta faɗa tare da zare hannunta ta mike tsaye "Matata mana.."
"Ka ɗauko ta? Tun ba a yi bikin tariyar.." Dakatar da ita ya yi. "Na faɗa miki na ɗaukota ne don kar sai gari ya waye ki ganta..."  Da ƙyar ta iya danne abin da ke ta so mata  kana ta ce "Na fahimta" Daga haka ba ta sake cewa uffan ba har ya gama zaman shi ya fita a ɗakin. Wani dogon tsaki ta ja tare da ɗaukar wayarta ta kira ƙawarta. "Alhj Aminu dai ya ɗauko wannan shegiyar matar ta shi, ya zo yana faɗa min ya taho da ita, sai ka ce ba ta da dangin da za su kawo ta" Dariya ƙawarta ta yi sannan ta ce "Ba rashin dangi ba ne ki fahimta, a yau babu uwar

da za ta ɗauki wannan iskancin a yi aure sama da wata takwas 'ya na zaune a cikin gida, ba na raba ɗayan-biyu ko dai yana lallaɓata suna shoshalewa ko kuma dai uwar ta fahimci wani abun shi ya sa suka ba shi ita ba tare da su sun kawota ba”

Laraba ta ce “An ya kuwa Aminu zai iya tarawa da ita a waje? Kai! Ba na jin zai yi haka..”
“Ban katse ki ba, amma ba a shaidar namiji musamman ma mijinki ke fa kike faɗa min yadda yake bin ki ba ya miki da wasa, a rana zai iya juye miki so biyar kar ki ji mamaki dan ya ɗauke ta sun fita holewa. Wancan karon ai tare suka yi tafiya ya dinga raina miki hankali ke ga ki shashasha kina zaune sake da baki mijinki na can yana shan madarar budurci...” Runtsa idonta ta yi tare da faɗin “Ya isa haka! Yanzu yaushe za ki koma wurin malam?” Wani mugun dariya Fumi ta yi sannan ta ce “Haba ƙawata barshi ya sha romon budurci kafin a datse masa jijiyar jin daɗi...”

“Ba fa zai yuwu ba! Tun yanzu nake so a shafe jijiyar a mayar da shi lagwali ya kasa taɓuka mata komai ba na so ya mu'amulance ta bare har ya sake ajiye wani ƙwan a duniya. Wallahi tun da ta aure min miji sai ta ɗanɗana kuɗarta wani jin daɗi, ko farincikin aure ba za ta taɓa jin shi ba, sai na datse duk wani farinciki..”
Ajiyan zuciya Fumi ta sauke sannan ta ce “Shi kenan za a miki yadda kike so sai kin turo da abin sadakar”
“Wannan ba matsala ba ce zan tura miki yanzu” Haka suka ajiye wayar.
Lokacin da ya koma ɗakin ya samu ta kwanta shima kwnaciyar ya yi tare da shigar da ita cikin jikinshi “Amnoor..” Ya kira ta murya can ciki, lamo ta yi a cikin jikinsa tana sauke ajiyan zuciya. Kanta ta manna saitin zuciyarshi tana saurarон bugun da zuciyarshi ke yi. “Amnoor zuciyarka na bugawa da sauri me ya sa?” Ta yi tambayar tare da shafo tsakiyar ƙirjinshi. “Duk sa’ilin da zuciyata take irin wannan bugun adadin soyayyarki da ƙaunarki sake ninkuwa take cikin zuciyata. Noor! Ina matuƙar son ki..” Wani ƙayataccen murmushi ta sakar mishi tare da kissing ƙirjinsa. “Hubby Amnoor, adadin soyayyar da nake maka baki ba zai iya faɗarsu ba, yadda ka ke ji na a ranka, yana da bambanci da yadda ni ma nake jinka a raina” Ta yi maganar tare yin fari da idanunta wadda ya sa shi kamo ta yana faɗin “Kamar ya ya?” Ya ce yana kwance igiyar rigan barcin da ke jikinta riƙe hannunshi ta yi tare da faɗin “Nawa ya fi naka..” Haɗiye sauran maganar ta yi jin yadda ya shafo ƙirjinta zuwa mararta. Bai samu damar zuwa babban fada ba, kasance kasala da wani ciwon kai da ya sauko mishi duk yadda ya so kasawa yai. Haka suka kwana yana matse da ita cikin jikinshi.
****
Cire mata hannun da ta yi tagumi Maman su ta yi cikin faɗa ta fara mata magana “So hauka ne? A kan wanda bai san ki na yi ba za ki kassara rayuwarki? Namiji kike yi wa kuka da ta yin kanki? 'Ya'yana suna da kyawun da za a so su, ko Nuriyya da babanku ya takura mata ba rasa samarin ta yi ba, kwarjininta ya sa maza ke ƙin zuwa inda take, dirin jiki da ƙiba kawai ta fi ki, kyau da fari kin fita don me za ki tsaya sai shi bayan ya ce miki yana da matar da take mutuwar son shi, shima kuma yana sonta. Ba ga samari nan suna bin ki ba..”
“Duk ba su yi min ba! Ni shi nake so Mamanmu ni shi kaɗai na ke so gabaɗaya kin kasa fahimta yanzu kin zama me zafi, kina magana cikin faɗa bayan da ba haka kike mana ba” Kwantar da kanta ta yi saman cinyarta tana shafawa “Firdausi rayuwa babu yadda ba ta juya mutum, ko ni ina mamakin yadda na koma mafaɗaciya, halayyar babanku na daga cikin abin da ya sa na koma haka, da kuma yadda 'yar'uwarki ta raina min hankali tana bin mijinta wani lokaci har

kwana take wurinshi a tunaninta ban fahimta ba, ba ta san na yi mata shuru ba ne..”
“Shi ya sa kika ce lallai sai ya ta fi da ita? Kin san ba ki kyauta mata ba, dan ɗazun ma sai da muka yi maganar da Amrah a kan yadda mijinta ya ɗauke ta ba tare da 'yan rakiya ba gaskiya ban ji daɗin hukuncin ba”
Maman Nafisa ta ce “Alhj Aminu shi ne wadda na yi aiki a gidansa, kin fi kowa sanin irin wulaƙancin da matarsa da 'ya'yansa suka min ai na ba ki labarin komai, shi ya sa na ce ya ɗauke ta su ta fi” Zaune Fiddoh ta miƙe tana faɗin amma Mamanmu me ya sa mijin Amnoor yake rawar jiki a kanta? Ki tuna lokacin da baba ya ɗauke wayarta still ya sake sayo mata wani ba tare da ɓata lokaci ba, yana girmama al'amuranku ke da baba, ki kalli yadda ya saya mana wannan gidan da muke haya ya dawo mallakin mu, sannan ya keɓance mana na mu ɓangaren ya gyara ya zuba komai na more rayuwa, ko akwai wani abu ne?”
Ɗan murmushi kawai Maman Nafisa ta yi tana faɗin “Abin a jininmu yake, duk 'yan gidanmu haka maza ke rawar jiki a kansu, muddin suka ji yadda abin yake..”
“Kenan akwai wani sirri na daban?” Fiddoh ta yi mata tambayar tana son tabbatar da akwai ɗin, domin irin hakan ta ganshi a karan kanta, yadda maza ke binta da zaran sun yi sau ɗaya haka za su ci gaba da bibiyarta gashi duk wulaƙancin da take musu suna shanyewa musamman ma Emanuel har yanzu ya kasa rabuwa da ita duk inda ya je haka zai dawo yana ba ta labari ba kamar ya ita ba, domin ita ɗin tana da wani baiwa na daban.
“Akwai amma ban san mene ne ba, na san dai namiji ba zai taɓa wulaƙanta min 'ya ba”
Miƙewa Fiddoh ta yi tana faɗin “To! Duk yadda zan yi sai na yi wurin ganin na mallake shi, kuma koma wacece matar shi ko matan shi sun shiga uku muddin mijinsu na shiga hannuna, ba zan bi boka ko malam ba, amma ƙissa da kisisina tare da duk wasu sheɗananci zan yi don mallake shi!”
“Allah ya kyauta Ubangiji kuma ya shirye ki, kullum girma kike amma har yanzu ba hankali, kina tsaye kina kallo na kike faɗar za ki yi duk abin da zai sa ki mallake shi? Kenan za ki kutsa kai inda ba a yi da ke?”
Fiddoh ta ce “Ko yana sona ko ba ya sona ni dai na ji na gani shi nake so..” Tana gama faɗar haka ta fita a gidan “Allah kai ka ba ni ita, Ubangiji ka shiryar da ita, Allah ka nutsar min da ita ta dawo gida ta zauna ta bar rayuwar da take” Addu'ar da kullum take yi wa Firdausi kenan, domin ba ta jin daɗin rayuwar da take yi musamman da mutane suke aibata ta, sai dai duk zagin da mutum zai yi mata bai isa ya kalli ƙwayar idonta ko ya tunkare ta da wannan maganar ba, domin tana iya illata mutum. Police kuwa sun santa dan abu kaɗan za ta sa a cilla mutum a cell. Mutane da yawa na shakkar ta dan ba ta ɗaukar iskanci yarinyar da uban da ya kawota duniya ma ba ta raga mishi ba wa za ta ƙyale?.
★•°•°•°•°★
Maƙontan su na cikin gida ne suka je mata jere duk da ya zuba mata komai amma haka Maman Nafisa ta shiga kasuwa ta yi mata sayayya domin yanzu kam Alhamdulillah suna samun kuɗi daga bangaren shi ma yana musu aike kama daga kayan abinci, atamfofi, da duk abin da za su buƙata, a hakan ma tana taka mishi burki domin hidimar ta yi yawa. Ta yi mata sayayya daidai gwargwado babansu kam ya ce sisi ba zai kashe ba, tun da ta zama mai kuɗin banza miji ya zuba mata komai amma tana nan tana kashe kuɗi sai ta yi ta yi. Dariya kawai ta mishi dan yanzu ba ta cika mishi dogon magana ba, amma in zai kawo mata wargi tana taka mishi burki wadda yanzu ya fara shakkar ta ganin ta zama masifaffiya. Kuɗi kam idan ya ƙyalla ido ya ga ta

ajiye cinikin turare kwashewa yake yi, in ta yi faɗar ta gaji haka za ta yi shuru, amma duk abin da ya danganci 'yar gaban gishinsa ba ya ma taɓawa sai dai ya sake adana mishi dan ta fi shi rashin daraja har cikin mutane take bin shi ta tsutsiye shi lallai sai ya dawo mata da abin da ya ɗauka, an yi haka ba so ɗaya ba, ba so biyu ba. Da ya ga lallai ta fishi sheɗanci tuni ya daina taɓa kayanta.

*°*°*°*•°

Ba ta fuskantar matsala daga matar shi suna zaune lafiya. Dan tare suke shiga kichin su yi aikin abinci sa'i da lokaci Suhaima ta kan kawo musu ziyara domin dai ya ƙi yarda ta dawo gidan ganin yadda Amnoor take da fara'a kuma suna zaune lafiya da mahaifiyarta ya sa ita ma ta sake har suke gaisawa da 'yar hira tana girmamata a matsayinta na matar mahaifinta domin sai da Hajiya Umma ta ja mata kunne sosai tare da gindaya mata kashedi na ba ruwan ta da Nuriyya bare ta ce za ta taya uwarta kishi, da ke tana tsoron kakar tata shi ya sa ta nutsu take mata biyayya. Yanzu tana ɗan fita yawon daren ta ganin Hajiyar ba ta takura mata Lil ne dai ya ƙi saukowa tun faɗar da suka yi da Fiddoh duk inda ta samu labarin yana zuwa bin shi take yi. Amma ko kallo ba ta ishe shi ba.
"Amnoor ya dai na ga kin yi wani yanayi na daban a kwai wani abun ne?" Ya faɗa tare da kamo hannunta, ɗan murmushi kawai ta yi tare da juyawa tana ƙoƙarin shafa mai towel ɗin da ke jikinta ya kai hannu zai kwance mata, ba ta hanashi ba, domin ta san ba abin da zai iya yi mata wanda ya wuce ya jagwal-gwalata tana jin shi ya fara taɓe-taɓe ita dai ba ta ce komai ba bayan shurun da ta yi. "Ki yi haƙuri wallahi ni ma ban san abin da ke damuna ba"
"Uhm ka ji na ce wani abu dangane da rashin kafiyarka? Ko na ce maka na gaji da.." Rufe mata baki ya yi da sauri yana faɗin "Baki faɗa ba, amma alamu sun nuna kina kewata ko? Na sani ni ma ina kewarki" Danne damuwarta ta yi tare da haɗe fuskokinsu kissing lips ɗin shi ta yi. "Hubby karka damu In Sha Allah za ka ji sauƙi"
"Kin tabbata babu damuwa?" Juyowa ta yi tana kallon shi tare da faɗin "In sha Allah babu komai" Jan karan hancinta yai tare da faɗin to ki gama shiryawa sai mu je asibitin tare ko?" Gyaɗa mishi kai ta yi, yana tsare har ta gama shiryawa kallonta kawai yake yana haɗiyar miyau shi dai wannan ciwon ya katse mishi jin daɗi. Har za ta shafa man baki sai ta ajiye domin ta san ko ta shafa haka zai lashe, yana riƙe da hannunta har wurin mota Hajiya Laraba ta rako su tana musu a dawo lafiya, motarshi na fita a gida ta kwashe da wani mugun dariya tana faɗin "Haka za ka yi ta gantalin neman magani ba za ka taɓa samu ba" Suna zaune gaban likitan da ta duba shi hannunshi na cikin nata ya ji likitan na faɗin "Alhj ni kam wannan lamarin naka yana ba ni mamaki, duk da an yi aiki a wurin kuma kana shan magani amma dai har yanzu fa sai a hankali..."
"Kamar ya ya sai a hankali?" Likitan ta ce "Batun iyalinka nake nufi sai..."
"Dalla dakata malama ban fahimce ki ba?" Kallon shi likitar ta yi ganin yadda ya fusata.
"Duk kuɗin da na ba ku? Ke kisan abin da nake ji kuwa? Matana biyu fa? Ki kalleta da kyau kina nufin haka zan zauna ina kallon ta da kuruciyarta?"

"Sau nawa kake yi? Kallon Amnoor ya yi sannan ya sake kallon likitar "A sati ko a rana?" Sunkuyar da kai na yi domin na fahimci a kan me suke maganar duk sai na ji kunya ta baibaye ni amma shi ko a jikinshi likitar ta ce "A rana"

“Ke sau nawa kike yi?” Ya wurga mata tambayar dan ya lura tambayar renin hankali take mishi “A'ah Alhaji ba ka ba ni amsar tambaya ta ba”
Riƙe mishi hannu na yi tare da matsewa ina mishi alamar rarrashi domin na lura ya fusata da maganar likitar. “Idan na faɗa miki adadin da nake yi a rana tsorata za ki yi, domin tun ba ta saba ba haka har ta saba tana nema da kanta, shi ne yanzu za ki faɗa min wani zancen banza ina ga ba ku san aikin ku ba ba zan iya zuba ido ina kallo mace ba tare da na juye mata abin da...” Riƙo shi na yi tare da faɗin “Ki yi haƙuri Dr tun da aka ce mafitsarar shi ya samu matsala yake a fusace, musamman ma idan aka ce ba zai iya tarawa da iyali ba” Na faɗa ina kallon ƙwayar idonshi “Ni na ce miki ba na jin ƙarfin da zan..”
“Mu je gida lokacin shan maganinka ya yi” Dariya kawai Dr ɗin ta yi domin daga shi har matar tashi dariya suke ba ta ganin yadda ta ɓata rai tana cewa su je ya sha magani shi kuwa sai faɗin “Ni na ce miki ba ni da ƙarfin da zan yi wani abu? Wato kin raina ni yanzu saboda kin ga ba ni da lafiya ko? Ya yi kyau!”
“Dan Allah duk wannan rigimar ka ajiye shi har mu ƙarasa gida tukun na lokacin ne zan kulaka amma ban da nan domin idon jama'a na kanmu” Suna ƙarasawa gida ya fisgota da ƙarfi kamar zai ɓalla mata hannu “Saboda ba ni da lafiya shi ne kike min haka? Kin gaji da ni ko kina son rabuwa da ni dan ba na biya miki buƙatar ki...” Hannunshi ta riƙe har cikin falonta Zaliha ta iske zaune. “Aunty Noor kun dawo? Daddy ya jikin ka? Na zo Maman Suhaima take cewa kun je asibiti” Da sakin fuska ya amsa mata sannan ya fita zuwa nashi ɗakin. Zama Nuriyya ta yi tana faɗin “Ai na manta yau za ki zo ga shi ban girka mana komai ba ko za ki shiga ki mana girkin?” Miƙewa ta yi tana faɗin “To” Kayanta Amnoor ta adana mata sannan ta nufi ɗakinsa yana kwance ta ɗauko magani da ruwa tana miƙa mishi karɓa ya yi tare da ƙure ta da ido, ɗauke kanta ta yi sannan ta miƙe ta fita a ɗakin.
Da yamma suka haɗu dukkansu a falo suna cin abinci suna kammalawa Laraba ta yi ɗakinta domin tun da Amnoor ta tare ta sallama mata shi tun da ta san abin da ta ƙulla musu. Kwana biyu Zaliha ta yi ta tattara ta ce za ta koma gida dan masifar da suke yi kullum dare ya ishe ta ɗan kullum da dare sai sun yi faɗa yau da wuri ma suka fara rigimar ta su. “Daddy mai ya sa kake min irin haka? Kana ganin ƙanwata na nan amma kullum sai ka ta da rigima ka bari ta koma mana in ya so koma mene ne sai ka yi tun da ka zama mafaɗaci..”
“Ni kike faɗawa wannan maganar? Amnoor zan mare ki...” Da mamaki ta matso tana faɗin “Daddy ai ba sai ka faɗa ba, daman na daɗe da fahimtar kana son kai hannu jikina wallahi na gaji da wannan fitinar naka haba dan Allah sai ka ce wani ƙaramin yaro kullum sai an jiyo muryan mu...”
Kallon hannun shi ta yi tare da faɗin “Shi kenan ka mare ni ko wutar da ke cin zuciyarka zai ragu” Fitowa ta yi a ɗakin zuwa nata ɗakin dan kusan sati basu kwnaciya tare tun da ya tsiro da faɗar dare. Kallon Zaliha ta yi tare da faɗin “Ke lafiya na ganki da jaka?” Zaliha ta ce “Aunty Noor gaskiya ni gida zan ta fi wallahi ba zan iya da diraman ku ba” Ɗauke hawayen da ke zubo mata ta yi sannan ta ce “Shi kenan ki gaishe da Mamanmu ki ce mata ina kewarta” A haka suka yi sallama. Zama ta yi tare da fashewa da kuka dan ta rasa abin da ke jawo musu wannan fitinar kullum dare babu kwanciyar hankali sai sun yi faɗa sun koma tamkar karnuka tun ba ta kula shi har ya fara kaita maƙura.

#Paidbook 500
09079740079
[5/9, 11:45 PM] FARHATULKALB💔🤗: *♡AMNOOR...!*
_A romantic story_
Wattpad: ayshajb
Arewabooks:ayshajb
®
FARIN JINI WRITER'S ASSOCIATION📚
★F. J. W. A★

Free page 33_34

Ku je YouTube ku yi Subscriber Channel ɗi na FARIN JINI HAUSA TV. Domin samun ƙayatattun littafanmu.

H-P Place Group.

“Ya Nuriyya suke.?” Maman Nafisa ta yi mata tambayar bayan ta ajiye jakar Zaliha da ta karɓa. “Gaskiya babu lafiya Maman mu, dan kullum Aunty faɗa suke yi da mijinta...” Dakatar da ita Maman Nafisa ta yi da faɗin “Hajiya Laraba ke haɗa su faɗar ko? Dan na san za ta aikata fiye ma da hakan in dai a kan mijinta ne..” Cikin sauri Zalihar ta katse ta da faɗin “Ko ɗaya Mama mu, ai Maman Suhaima tana da kirki kuma suna zaune lafiya sai ma kinga yadda suke komai tare tamkar ma ba kishiyoyi ba tsakaninta da Daddy ne ban san me ke faruwa wanda kullum yake haddasa musu rigima ba” Shuru Maman Nafisa ta yi tana juya zancen a ranta ta san muddin Nuriyya ta ce ta yi kewarta tabbas tana cike da damuwa mai tarin yawa ne. Yinin ranar haka ta yi shi zuciyarta cike da tunanin ɗiyar tata, da a ce Fiddoh za ta amince da ta kaiwa Noor ɗin ziyara amma ta san da kamar wuya. Aikuwa Fiddoh na dawowa ta tare ta da maganar buɗar bakinta sai cewa ta yi “Ni in je gidanta? To in yi mata mene?” Da ga haka ba ta sake cewa uffan ba, domin zancen ma ɓacin rai yake saka ta.

Amnoor kuwa shuru ta zauna a ɗakinta tana tunanin abin da ke haddasa rigima tsakaninta da mijinta sai dai duk iya bincike da ta yi ba ta gano komai ba, ƙarshe haka ta kwana da matsanancin ciwon kai, ko da ta farka da Asuba da ƙyar ta iyayin sallah ba ta samu damar yin azkhar ɗin da take yi kullum ba haka ta kwanta tana riƙe da kanta. Rashin jin motsinta ba ƙaramin damunsa yai ba, domin ta saba zuwa duba shi ko da ba su kwana wuri ɗaya ba. Ga shi ko abincin kari bai ga alamar za ta kawo mishi ba, an ya ma ba fushi ta yi da shi ba? Tambayar da ya yi wa kanshi wanda ba shi da mai ba shi amsar kenan. Haka ya yi wanka ya shirya ya fito ɗakin Laraba ya leƙa nan ya ga ba ta nan, tun da ya doso ɗakin yake jin yadda take nishi tare da sheshsheƙan kukanta, da sauri ya ƙarasa ganinta yai dafe da kai tana juyi ga hawaye da ke zariya bisa kuncinta “Ya Subahanallah Amnoor!” Ya kira sunanta cikin rikicewa yana ɗagota “Mene ne? Ina ke miki ciwo? Daman ba ki da lafiya shi ne ba ki kira ni ba?” Duk wannan tambayar ya jero mata lokaci ɗaya. Da sauri ya ɗauki waya tare da kiran likita yana faɗin ta zo cikin gaggawa. Babu ɓata lokaci kuwa likitar ta ƙaraso kafin zuwan likitar ya yi ƙoƙarin ba ta tea. Nan ta yi mata allura  domin jikinta har da zazzaɓi magunguna ta ajiye tare da faɗa mishi yadda

za ta sha su sannan ta ƙara da faɗin “Damuwa ya yi wa Madam yawa, ya kamata a kiyaye abin da zai dinga haddasa mata wannan damuwar” Tana gama abin da za ta yi ta yi tafiyarta.

Yana zaune jikinta har ta farka “Sannu Amnoor yaya kike jin jikin yanzu?” Ɗan murmushi ta sakar masa tare da daurewa ta ce “Ya yi sauƙi, ya naka jikin? Ka sha magani yau?” Ta yi maganar tana ƙoƙarin ta shi zaune. “Na sha kuma na ji sauƙi sosai” Miƙewa ta yi ta gyara ɗakin sannan ta nufi toilte ta wanke duk inda ta gifta yana binta da ido cikin zuciyarshi yana jinjina ƙarfin hali irin nata har ɗakinsa sai da ta je ta gyara ko’ina sannan ta shiga kitchen ta yi musu girki. Haka ta dinga daure ciwon kan da yanzu yake takura mata tana aikinta izuwa yanzu rigimar tasu yai sauƙi batun kwana gado ɗaya ne dai har yanzu babu in ya fita aiki yana ƙoƙarin dawowa da wuri kasancewar tana cikin kaɗaici yanzu ita ɗaya a gida a hakan ma wani lokaci Amrah na kawo mata ziyara wacce ita ma yanzu karatu take gadan-gadan ba kama hannun yaro shi ya sa ba ta samun zuwa wurin Amnoor ɗin.
Cikin barci ta fara jin warin hayaƙi buɗe idanunta ta yi tana kallon yadda tsakiyar ɗakin ya turniƙe da hayaƙi babu jimawa ta fara jin sautin dariya na muryoyi daban-daban wani irin juyawa ta ji kanta na yi dafe kunnuwanta ta yi da duka hannayenta tare da runtsa ido. Gabaɗaya ta mance da addu'ar sai jujjuya kai take tana runtsa idanu. Kimanin mintuna talatin ana haka kafin ta ji komai ya ɗauke zubewa ta yi a ƙasa tana mayar da numfashi daga haka barci yai awon gaba da ita. Ko da gari ya waye ta kasa faɗa mishi abin da ya faru, shi kuwa kasa shuru ya yi ganin yanayinta kamar a firgice take, ya yi mata tambaya sai dai ta ce babu komai, haka ya ƙyaleta ba don ya yarda ba. Yana kammala shiryawa ya fita aiki. Tun bayan fitar shi al'amarin jiya  ya dawo, na yau ma ya fi na jiya tsananta domin wuni aka yi ana firgitata duk inda ta juya sautin ihu da dariya ne ke kaiwa kunnuwanta farmaki ga shi ta kasa furta kalma ɗaya na addu'a sai gab da magariba ta ji gidan ya yi ɗif tamkar ba shi ne ya ke juyawa ba juyowan da za ta yi ne ta yi arba da shi yana tsaye, da gudu ta nufeshi ta rumgumeshi tana fashewa da wani irin kuka, sosai ta yi kukan shi ma bai hanata ba domin ya lura tana cikin damuwa sai da ya ga kukan ba mai ƙare wa ba ne ya shiga rarrashinta washegari ma yana fita gidan ya juye mata zuwa wani sansanin daji na daban. Kwana biyar tana cikin firgici da tashin hankali wanda ta rasa da wane yanayin za ta yi masa magana ya fahimce ta. Gabaɗaya ta rame ta susuce tare da fita a hayyacinta. Bata iya taɓuka komai yanzu hatta abinci ba ta iya girka musu sai dai ya sayo musu. Shi kanshi yanayin da take ciki na damunsa amma da zaran ya tambaye ta sai dai ta ce bakomai so biyu yana kaita gidan Hajiya Umma a nashi tunanin ko zama ita ɗaya ne ke sanyata cikin damuwa amma duk da hakan ba ta dawo yadda take da ba. Yana cikin shirin tafiya aiki ta kalleshi tare da faɗin “Daddy ina so inga Maman mu” Jakar shi ya ɗauka tare da faɗin “Bari in na dawo anjima sai mu je tare” Sunkuyar da kai kawai ta yi domin ta san muddin suka tafi tare ba wani daɗewa zai barta ta yi ba.

Ya fito daga Ofishin sa kenan sakataren shi ya kira shi yana sanar da shi baƙin su sun iso dole ya shi ne ya nufi filin jirgi domin tarban su, da ga nan ya je ya kama musu masauki a tsattsaye ma suka gaisa domin gabaɗaya tunaninsa ya yi gida ganin har bakwai saura yau bai je gida ba, ga shi ita ɗaya ce a gidan. Da hanzari ya fito yana kallon wayarshi da ke haske alamar shigowar saƙo kasancewar ya saka wayar a silent nan ya ga miss call haɗe da saƙonninta tana tambayar lafiyarshi da abin da ya hanashi dawowa gida. Mayar da wayar yai cikin aljuhunshi tare da buɗe motar yana ƙoƙarin shiga. Da ga bayan shi ya ji an dafa kafaɗar shi da mamaki ya juyo yana

tunanin waye haka? Nan ya yi arba da ita wani dogon tsaki ya ja tare da sake tamke fuska cikin ɓacin rai ya cire hannunta a jikinshi yana binta da ƙasƙantaccen kallo ganin irin shigar da ke jikinta wanda gabaɗaya ya bayyana komai na jikinta kasancewar kayan ɗamammu da su. “Alhaji na...” Wani irin zubewa ta yi a jikinshi gabaɗaya tare da fashewa da wani mugun dariya da ga haka idanunta ya fara rufewa Emanuel ne ya ƙara so wurin da sauri tare da ɗaukar ta yana faɗin “Yi haƙuri Alhaji ta yi sama sosai” Saboda tsananin takaicin kwanciyar da ta yi cikin jikinsa kasa magana ya yi. Haka ya ja motar yana me jin ƙyanƙyamin jikin nasa har ya ƙara sa gida.

Ajiyar zuciya ta sauke tare da miƙewa da sauri ta taho ta amshi jakar da ke hannunsa “Barka da dawowa Amnoor” Lumshe mata ido ya yi tare da jinginuwa da ƙofar shi ma yana sauke numfashi “Ki yi haƙuri yau ban dawo da wuri ba” Ɗan murmushi kawai ta yi tare da riƙo hannunshi zuwa d'akinshi. Sai da ya yi wanka tare da yin sallah sannan ta kawo mishi abinci tare da magani, kaɗan ya ci sannan ya sha maganin, kwashe kayan ta yi ta mayar da su kitchen kana ta nufi ɗakinta, wanka ta yi ta fito ɗaure da zani ba ta san yana ɗakin ba sai da ta ji ya yi gyaran murya sannan ta waigo tana mamakin zuwan nasa kasancewar yanzu bai fiya shigowa da dare ba. Karɓan man da za ta shafa ya yi tare da jan zanin nata gefe kawa kawai ya ji yana son rage ma kanshi zafi da ita bayan tsawon lokaci da suka ɗauka ba tare da wani abu ya shiga tsakaninsu ba, duk wanan sheɗaniyar yarinyar ce ta saka shi cikin wannan halin (Fiddoh) haka ya fara bin santala-santalan cinyoyinta yana shafa mata mai cikin wani irin yanayi kasa daurewa ta yi da sauri ta riƙe hannunsa tare da girgiza mishi kai. Wani irin kallo yai mata sannan ya kwance zanin gabaɗaya ya jawota cikin jikinshi sannan ya kashe hasken ɗakin, nan ya dinga birkita mata lissafi wanda har kuka sai da ta yi mishi domin ya kunnota da ga ƙarshe sai ya kasa yi mata komai takaicin wannan abin ya sa ta juya mishi baya, shi kuwa a rayuwa ya tsani irin haka wai su kwana gado ɗaya kuma mace ta juya mishi baya.

Haka rayuwarsu ta ci gaba da tafiya zaman lafiya ya yi ƙaranci a tsakaninsu tamkar masu almatsutsai yanzu-yanzu za su yi magana cikin daɗin rai ba jimawa kuma za su fara faɗa. Wannan abin shi ya sake ƙara mata damuwa sosai, yau yana fita  ta haɗa kayan da za ta buƙata ita ma ta nufo gida lokacin da ta zo Maman su na aikin turarenta ta yi sallama da ’yar siririyar muryanta tare da zama jikin Maman Nafisa tana sauke ajiyan zuciya nan da nan ta ji wani nutsuwa ya zo mata take ta fara barci shafa kanta Maman Nafisa ta yi tana ƙare mata kallo ganin yadda ta sukurkuce ta lalace duk ta rame, gyara mata kwanciya ta yi sannan ita ma ta ci gaba da aikinta sai zuwa ƙarfe biyun rana ta farka za ta yi magana Maman Nafisa ta ce “Yi addu'a tukun na” Lumshe ido ta yi tare da karanto addu'a. Ruwan rubutun da ta sa Zaliha ta amso mata wurin malamin makarantar su tun kwanaki ta ɗibo tare da miƙa mata. “Ki sha da Bisimillah” Haka kuwa aka yi tana gama sha ta dire kofin tana sauke ajiyan zuciya.

“Me ke faruwa?” Maman su ta yi mata tambayar tare da ƙura mata ido, sunkuyar da kai Amnoor ta yi domin ba za ta iya kallon maman tasu ba bare har ta faɗa mata abin da ke faruwa ba. Ganin yadda take matse 'yan yatsun hannunta ya sa Maman fahimtar ba faɗa mata za ta yi ba, daman ta san halin kayanta da ƙyar ta iya faɗar damuwarta. Cikin jin haushin halayyarta Maman su ta ce “Ki tashi ko koma ɗakin ki...” A sukwane ta d'ago idanunta cike da hawaye tana

faɗin “Dan Allah..” Dakatar da ita Maman Nafisa ta yi da faɗin “Ba za ki zo ki tasa ni a ga ba kina min hawaye bayan na tambaye ki damuwarki kin ƙi faɗa min ba, gwara tun wuri ki tattara ki tafi, shin mijin naki ya san kin fito?” Girgiza mata kai ta yi alamar a'a shigowar Zaliha ya sa ta yin shuru tare da miƙewa “Wayyo Aunty Noor ke ce a gidan mu yau? Dan Allah Aunty ba ni wayarki in yi abu” Miƙa mata wayar ta yi tare da shegewa ƙuryar ɗaki tana kuka. Ita dai ba za ta koma gidan Alhj Aminu ba, gwara ta zauna gidan su wurin Maman Nafisa kawai.

A gajiya ya fito daga motar domin yau gabaɗaya bai huta ba saboda ayyuka da suka mishi yawa, da sallama ya turo ƙofar falon yana me kiran sunanta domin ya saba da in ya dawo tana zuwa karɓan jakarshi ko kuma ta rumgumeshi tana mishi oyoyo yau kuma sai ya ji shuru ɗakinta ya nufa yana tunanin ko dai sallah take nan ma bai ganta ba toilte ɗin ma shuru gaban madubin ya ga takardan da ta rubuta mishi saƙo. “Ka yi haƙuri na fita ba tare da izinin ka ba, Daddy na gaji ba zan iya ci gaba da zama da kai a haka ba. Rayuwa haka muna matsayin ma'aurata sam babu armashi a lokacin da ban saba ba kai ka sabar min, tun ba na jin daɗi har ka koya min jin daɗin, tun ina gajiyawa har na zama gwana. Ta yaya zan zauna bayan ina jin mararin abun? Akwai cutarwa sosai, na yi iya haƙurin da zan yi dan Allah ka fahimta. Ina mai roƙon ka da ka sawwaƙe min kawai dan ba zan iya zama kullum muna faɗa da junan mu ba” Lumshe ido yai yana jin wani zafi a ranshi da ƙyar ya iya yin wanka tare da sallah sannan ya nufo gidan na su.

“Kin wani kwaso jiki ke kin dawo gida to uwar me kika zo yi? Kin san dai halin baban mu wallahi in ya fara miki tijara ko ƙala ban cewa, haka kawai kin bar gidan mijinki kin zo kin tasa mutane a gaba kina cika mana kunne, an tambaye ki me ye matsar kin ƙyale mutane to me za a miki?” Cikin faɗa Fiddoh take mata magana domin ta ɓata mata rai, dan tana kwance tana jin maganar da Maman Nafisa ke mata. Kallon Fiddoh Amnoor ta yi hawaye na ci gaba da tsiyayo mata “Shi kenan duk cikin ku babu me lallashi na...” Saukowa Firdausi ta yi daga saman gadon tana faɗin “Lallashi? Ke yarinya ce da za a lallasheki?” Da ga haka ta ja dogon tsaki tare da shigewa bayi tana mita ita ta hanata barci. Tana fitowa ta karɓi wayar Maman su ta kira Amrah dan ba zai yuwu Amnoor ta zauna musu a gida bayan kuma da aurenta ba. “Ki zo ki tattara ƙawarki ta koma ɗakin mijinta tun ɗazu ta zo ta hana mutane saƙat da kukan banza”

Ajiye wayar ta yi tana kallon Nuriyya duk da zuciyarta cike yake da tausayin 'yar'uwartata amma ba ta ji za ta lallasheta bayan ba ta faɗa musu damuwarta ba. Suna zaune sai ga Amrah ta yi sallama ta shigo gaisawa suka yi da Maman su sannan ta nufi wurin Amnoor “Aminiyar me ke faruwa ne?” Ta faɗa tare da kwantar da kan Amnoor ɗin saman kafad'arta. “Amrah sun kasa fahimtar halin da nake ciki..” Da sauri Amrah ta ce “Haba Noor, ta yaya za su fahimta bayan ba ki musu bayani ba. Daddyn nawa ne ya miki wani abun bayan rashin jituwan da kika faɗa min kwanaki?”
“Amrah ni na gaji ne wallahi ba zan iya zama..”
Zaro ido Amrah ta yi tana faɗin “Innalillahi Noor! Me ya yi zafi haka? Da bakin ki kike cewa kin gaji da zama da Daddy me ya miki?” Kallon Amrah ta yi sosai a hankali cikin rawar murya ta fara sanar da ita halin da take ciki tun da ga kan rashin lafiyarshi da faɗar da suke yi har gane-ganen da take yi. Duk hirar da suke Maman Nafisa tana zaune tana jinsu, ita daman ta

san Hajiya Laraba ba za ta taɓa ƙyale Nuriyya da mijinta ba, ta yi shuru ne kawai lokacin da Zaliha ta zo take yabon halayyarta ita ta san wace ce Laraba ta san baƙin kishinta ashe dai zagon ƙasa take yi wa Nuriyya, aikuwa ba za ta ƙyale a kassara mata ɗiya ba.
Ɗakinta ta shige ta barsu suna ci gaba da tattaunawa, Amrah ta ce "Ikon Allah! Wannan lamari da ɗaure kai yake na ma rasa abin da ma zance wallahi" Zaliha ce ta miƙo mata wayarta da ake kira tun ɗazu. "Aunty Noor ana kira" Kallon Amrah ta yi tare da mata nuni da wayar "Ki ɗauka mana" Girgiza mata kai kawai na yi domin ban san abin da zance mishi ba. Ƙarshe ma kashe wayar na yi gabaɗaya ina ji kamar ban kyauta mishi ba, na san yana can cikin damuwa amma haka za mu yi haƙuri da juna. "Ki yi haƙuri Noor, zai fi kyau ki koma ɗakin ki, kin ga azumi na gabatowa bai kamata ki bar shi shi kaɗai a gida ba.."

"Ai ba ni kaɗai ba ce, Amrah zama na da Amnoor babu wani armashi, ko gado ɗaya ba mu kwana bare a kai ga batun biyan buƙata, babu fa abin da yake tsinana min kullum sai dai ya yi ta laguda ni yana ɗaga min hankali da ga ƙarshe ya barni da ciwon mara ina juyi ni ɗaya..."

Cike da kunyar zancen nata Amrah ta rufe bakinta tana faɗin "Tabɗi! Amnoor daman za ki iya wannan maganar? Lallai an kai ki maƙura tun da har kika iya faɗar wannan maganar. Ni wallahi har kunya ya kamani" Girgiza kai kawai Na yi domin ni ma sai da na yi maganar na dawo ina jin kunyarta.

"Za mu canza Please a dai yi haƙuri kamar yadda aka fara a ƙarasa bai kamata Daddy ya yi azumi shi ɗaya babu iyali ba, kin ga tun da Mommy ba ta nan ya kamata ke ki zauna dan ita daman tun asali ba zama take ba, tana harkan business ɗinta"

Shi kuwa ganin ba ta ɗauki kiran ba ne ya sa shi juyawa ya nufi gidan Hajiya Umma yana sanar da ita abin da ya faru. Shuru kawai ta yi masa domin ba ta san me za ta ce masa ba, saboda takaici wai ya zo ya zauna yana faɗa mata matarsa ta yi yaji to uwar me za ta mishi?.

A ɓangaren Hajiya Laraba kuwa murmushi kawai ta yi tana sauraron maganar da Maman Amrah take faɗa mata. "Wallahi ki ji tsoron Allah ki bar 'yar mutane ta yi zaman aure tun da ke ba auren ba ne a gabanki na rantse ko kaffara ba zan yi ba da sa hannun ki a duk matsalolin da Nuriyya take fuskanta tsakaninta da Alhaji Aminu dan na san halin baƙin kishin ki, duk wani dariya da rashin damuwa da kike nunawa duk a fuska ne bai kai zuci ba! Koma dai mene ne akwai Allah kuma gaskiya nake faɗa miki ki ajiye duk wani business ki dawo dan watan ibada za mu shiga" Dariya kawai ta yi tare da faɗin "Allahu akbar! Sannu fa na gode" Da ga haka ta kashe wayar tana jan tsaki.
"Ai ba ta ga komai ba ma, ba de ta ce mijina ba? Sai na haukata 'yar banza!" Da ga haka ta ɗaga kiran Hisham wanda yake damunta da maganar dawowarsa nan ta sauke mishi kwando bala'i kafin ta kira Suhaima tana tambayar lafiyarta.

Kwana biyu kenan da dawowata gidan mu Fiddoh kuwa ta saka ni a ga ba da bak'ar magana ita dai haushin dawowata take ji takan ce min "Ki ba ki ji daɗi ba ma Allah ya ba ki miji me ƙaunar

ki yana ririta ki, ni ga shi neman Alhaji nake yana wulaƙantani sai ce min yake yana da matar da ta fini komai" Ire-iren maganar da take faɗa kenan wanda sai dai in jita amma ban ce mata komai, ina mata addu'ar idan shi alkairi ne a gareta Allah ya haɗa su domin ba na son rayuwar da take yanzun abin nata ma ya daɗe lalacewa dan shigar nuna tsiraici take tamkar ba ɗiyar musulma ba, in na yi magana ƙarshe sai dai faɗa ya biyo baya. Maman mu kuwa ƙala ba ta cewa dan ta yi magana ta yi nasiha ta gaji sarautar Allah kawai zuba ma ido. Zaliha na kalla ina tambayarta baban mu domin tun zuwa ta ban ji motsinsa sa.

"Tab! Ai tun da Daddy ya ba shi jari yanzu linƙafa ta ci gaba. Yana can yana harkan caca be ma zaman gari sai dai ya kira mamar mu a waya kawai"

"Ya Subahanallah! Maimakon ya kama wani sana'ar da za ta amfane mu shi ne sai caca?" Na faɗa ina kallon maman mu da take miƙo min ruwan rubutu. "Karɓi ki sha da Bisimillah in kin gama ki shiga ba yi ki yi wanka na ajiye miki ruwan maganin" Da ga haka ta miƙe ta fita.

Haka Maman mu ta dinga cusa min wasu magunguna na tsarin jiki tare da na karya sihiri na sha da wanka, da kuma hayaƙi, sannan ta shiga min gyara na musamman kwana na goma muka ɗauki azumi ranar farko da aka fara azumi Daddy ya aiko mana da kayayyakin buƙata. ranar da muka kai azumi biyar Abban Amrah ya zo gidan mu shi da Hajiya Umma, ban san abin da suka tattauna shi da Maman mu ba kasancewar har yanzu baban mu bai dawo ba, na ga dai ta shigo ta ce min in shirya in koma gidan Daddy. Wani irin fad'uwar na ji da sauri na kalleta zan yi magana ta ce "Ki yi haƙuri watarana komai zai wuce ki riƙe ibadarki ki dinga zama da alaula ko da ba ki da tsarki Allah yana tare da ke kuma shi zai kare min ke, ga wannan ruwan rubutun ki yi ƙoƙari ya sha in Allah ya yarda magana rashin jituwa za ta kau, maganar rashin kwana wuri ɗaya duk zai wuce, zai kasance tare da ke. Sannan ki kula da tsaftar jikinki, kwalliya, sanya kayan da zai ja hankalin shi, ba wai kullum za ki dinga yawo cikin atamfa da leshi ba ne, akwai kayayyaki na zamani wanda za ki dinga sakawa mijinki a gida ki lura inda ya fi so, nan wurin shi za ki dinga gyarawa imma tafiyarki ne, ko magana, ko wani abin da ya danganci jikin ki ne, duk ki san yadda za ki jawo hankalin shi" Duk wannan maganar da take idanunta na gefe ko kallon inda nake ba ta yi. "Allahu akbar! Gaskiya mamar mu kin burge ni anan, sai yanzun kika samu damar faɗa mata abubuwan da suka dace ta yi a matsayinta na matar aure, ina fatan ni ma randa nawa ya tashi za a faɗa min fiye ma da haka..." Girgiza kai Maman Nafisa ta yi tare da faɗin "Ubangiji Ya shiryar da ke"

Zaliha ce ta fito min da kayana a wurin mota na tadda Hajiya Umma durƙusawa na yi ina gaisheta domin ba ƙaramin girmamata nake ba kasancewar tana sona ba ta taɓa nuna min wani hali na daban ba. "Taso-taso ɗiyar kirki. Allah Ya shiga lamarin ki, ki ƙara haƙuri da Aminulllah kuma zan ja mishi kunne kar ya yarda ya sake miki abin da zai sa ki dawo gida, kodayake hakan ma ya yi min tun da ya ɗanɗana zaman gwauranci mata biyu duka babu ko ɗaya. Yanzu dai na san za a kula da shi" Ɗan murmushi na yi ina sunkuyar da kaina na fahimci tana son cewa na kular mata da shi ne duk da ba ta fito ta faɗa min ba. Gidanta muka fara zuwa a can  muka taho tare da shi ashe yana can yana jiran zuwan mu. Tana fita a motar ya shigo tare da kama hannuwana yana sauke ajiyan zuciya, kissing hannuwana ya yi yana faɗin "Ki yi

haƙuri Amnoor...” Gyaran murya Abba ya yi tare da faɗin “Ai ka bari mu ƙarasa gida wannan rawar jikin duk na mene ne?” Hararan shi Alh. Aminu ya yi yana faɗin “Amma fa kai ɗan iska ne Sa’id , ban son sa ido fa”

“Au haba? Abin da za a saka min da shi kenan bayan na yo maka biko ko?” Haka suka dinga hira har kuma ƙaraso gida. Ciki na shiga na barsu suna tattaunawa, gidan ya yi fes ga dukkan alamu ya sa an gyara ne, haka ma ɗaki na shi ma a gyare yake har da ƙarin wasu abubuwan ma. Ba yi na shiga na yi alaula tare da gabatar da sallar Asham. ina cikin sallah ya kwaso kayan da na bari a mota ya shigo min da su, zama ya yi har na sallame tare muka shafa addu'ar tare da faɗin “Allahumma Amin Allah Ya sa ni dai an haƙura” Kala ban ce mishi ba haka na tashi na gyara kayayyakin sannan na ce “Wannan maganinka ne, maman mu ta ce a ba ka”

“To ina godiya”

Kwanciya na yi na barshi zaune. Shi kuwa kallonta kawai yake ganin yadda take wani basarwa maganin ya sha sannan ya nufi ɗakin shi ya shirya ya zo ya kwanta kusa da ita. Kasa haƙuri ya yi ya jawota jikinshi yana sauke ajiyan zuciya a haka suka yi barci ƙarfe uku ta farka tare da zare jikinta a nashi ta haɗa musu abin da za su yi sahoor. Ba ta wani sake mishi haka suka ci gaba da zama har aka kai azumi ashirin gabaɗaya ya yi wani yanayi ba ya jin daɗin sauyawan da ta yi, ko 'yar hirar ba ta ba shi fuskar da za su yi.

Kasancewar yanzun bayan sallar la'asar yake dawowa gida ne ya sa wani lokaci sai dai ya zauna yana kallon yanda take kai-komo daga kichin zuwa falo tana shirya musu abin buɗa baki. Yau tun da ya tashi yake jin shi a takura domin ko da asuba ya so ya lallaɓata ko zai rage wani abun amma ganin irin yadda take ɗauke mishi kai sai ya ƙyaleta kawai. Tana gama shirya komai ta nufi toilte dan yin wanka ganin shida har ya yi yau ba ta kammala aiki da wuri ba.

